


# KUNDIN TSARIN MULKI




**GABATARWA.**

Jam’iyyar youth party wadda ta qunshi kungiyoyi da sauran jama’a, na da zummar yin aiki ne ta fuskar hada kan ‘yan Najeriya. Muna da manufa ta kawo ci gaba da kyautata matsayin rayuwar ‘yan Najeriya baki daya.

Yanayi da tsarin tafiyar da madafun ikon hukumonin gwamnati da dimbin albakatun qasa da Allah ya huwace wa qasar nan, sun zamo hanyar kawar da talauci da inganta kadarorin dukiya a Najeria, a baya. Amma, a yanzu, abin ya koma son zuciya da kare muradu na qashin kai, a maimakon na qasa.

Ana son Mulki ne, ba don kawo ci gaban qasa ba, sai don kwadayin azurta kai da tara dukiya, yin hakan ya haifar da wagegen gibi tsakanin masu arziqi da talakawa. Babban abin damuwa ma, shi ne yadda talaka ya rasa kulawar da ta kamata, ta fuskar samun kayayyakin kyautata rayuwa, kamar ingantattun ayyukan kula da lafiya da gidaje da ingantaccen ilimi. Jam’iyyar Youth Party na da ra’ayin cewar, shugabanci na gari ne kadai, zai kawo sauyin da ake buqata na maida Najeriya sabuwar qasa.

Kazalika, kwadayin Mulki da son tara dukiya fiye da kima, don kare muradu na qashin kai dana iyali a tsakanin wadanda ke rike da madafun iko, ya kawo koma baya ga tafiyar da tsarin demokaradiya. Wannan dabi’ar, ta sa masu rike da madafun iko, ba sa barin a samu daidaito don gudun sauka daga Mulki.

Dalilin hakan, ya sanya ‘yan siyasa ke shakulatin bangaro da gudummawar da ya kamata su bayar wajen tafiyar da tasrin demokaradiyya, a maiamakon haka, sai suke maida hankali ga abin da tsarin demokaradiyyan zai samar masu; hakan ke jagorancin fadawa ayyukan cin hanci da rashawa da mulkin qarfi da yaji da nuna halin ko in kula ga ci gaban qasa da tsarin demokaradiyya.

Jam’iyyar matasa ta (Youth Party) ta daura dambar tabbatar da shugabancin gaskiya da adalci da daidaito, da mabiyanta za su rinqa kaucewa siyasar kudi da rashawa da cin hanci da rikice-rikice da aringizo.

Bayan haka, akwai qarancin fahimtar bangaren adawa a qasar da demokaradiyya ta zama gasa; inda bangarorin hamayya na Jam’iyyun siyasa ke yi wa juna kallon kallo, a maimakon daukar juna da mahimmanci ta hanyar hada hannu wuri guda don tattauna muhimman abubuwan bunqasa tattalin arzikin qasa, haka, ta sa ake samun ballewar wasu

jiga-jigan 'yan siyasa daga jam'iyya, su koma 'yan tawagar kawo koma baya ga ayyukan gwamnatin da ke Mulki, daga nan sai rashin tsaro da hadin kai da zaman lafiya su wanzu, tsarin tafiyar da gwamnati ya kidimce. Daga nan ne, fa, hamayya tsakanin qungiyoyin Qabilu da jihohin da ke da yawan Jama'a za ta yi zafi. inda kowa zai duqa fafutukar neman rayuwa mai gwabi. A bisa wadannan dalilai ne, muhimman mutane masu fada aji a qasar nan ke qaurace wa harkokin siyasan tare da barinta a hannun 'yan siyasan bani na iya.

Sai ga shi, a yau, dattawan da suka Mulki qasar nan tun a matakin shekaru ashirin da talatin, ke ci gaba da jan akalar siyasar Najeriya, duk da sabanin ra'ayoyinsu da tsohon salon da suke amfani da shi wajen kyautata makomar qasar nan.

Har yanzu, matasan qasar nan, basu da kimtsin da za su iya jan ragamar harkokin siyasar fiye da tsoffin 'yan siyasan ta la'akari da tabarvarewar da qasar ta yi.

Qasar nan, na buqatar shugabannin siyasa masu jini a jika, masu kaifin basira da hangen nesa da hikimar tafiyar da ayyukan gwamnati da jajircewa da sadaukar da kai wajen maido da martabar qasar nan, ta fuskar tabbatar da gaskiya da adalci da ci gaba da kauda cin hanci da rashawa da duk matsalolin da ke tauye bunqasar qasar nan.

Jam'iyyar Matasa ta (Youth Party) ta himmatu, wajen tabbatar da hadin kai da yi wa 'yan Najeriya aiki ta bin sahihan manufofin tsarin demokaradiyya. Babu shakka matasan Najeriya sun nuna qwarewa a bangarorin ci gaban al-umma da sana'o'i da sauaran harkokin da suka jibinci shugabanci. Amma duk da haka, gurbin da suke da shi na zama kan gaba wajen ba da gudummawa ga harkokin siyasa, ya yi kadan.

Jam'iyyar matasa ta (Youth Party) na qoqarin kawo sauyi a ta wannan fuskar tare da hadin kan matasan Najeriya, qarqashin manufa daya ta gina sabuwar Najeriya.

## MANUFOFI DA QUDURORI

a. Ba da gudummawa da inganta tsarin demokaradiyya a matsayin jagorar tafiyar da mulkin qasa, ta hanyar kaucewa rikici da siyasar cin hanci da bita da qulli.
b. Don samar da daidaito a tsakanin jama'a, don rage gibin da ke tsakanin mai arziki da talaka, wanda ke haifar da rashin tsaro da samar da abubuwan bukata na kyautata rayuwa, musamman, ingantattun ayyukan kula da lafiya da gidaje da nagartaccen ilimi ga talakawa.
c. Samar da shugabanni na gari masu kaifin tunani da hangen nesa da dabaru, da za su kare muradun qasa da yi wa jama'a aiki, wadanda za su sadaukar da kai wajen maido da martabar qasar nan, ta hanyar kawar da ayyukan rashin gaskiya da cin hanci da rashawa.
d. Da ba da gudummawa a bangaren qoqarin da ake yi na bunqasa tattalin arziqin Najeriya, a lokacin da Jam'iyyar ba ta kan qaragar mulki.

e. Qarfafa gwiwar matasan Nigeriya don shirya kansu ga tunkarar harkokin siyasa don sanin madosa.
f. Don samar da sabuwar Najeriya mai martaba da qima a idon duniya da za ta tabbatar da gaskiya da adalci da kishi da jajircewa da sadaukar da kai wajen bi da kiyayewa da qa'idoji da sharuddan dokar tsarin shugabanci, don kayautata rayuwar 'yan qasa.
g. Da samar da daidaiton madafun iko tsakanin gwamnatocin tarayya da jihohi da qananan hukumomi a kan tsari na jamhuriyyar tarayya.

SABO DA HAKA, MU 'YA'YAN JAM'IYYAR (YOUTH PARTY), Bisa manufofi da qudurorin jam'iyyarmu, za mu tabbatar da kykkyawan shugabanci da mulki na gari, don haka….

MU KA SAMAR WA KAN MU DA WANNAN KUNDIN TSARN MULKI KAMAR HAKA.

**BABI NA DAYA**

TANADE-TANADEN KUNDIN TSARIN MULKIN JAM'IYYAR NA BAI DAYA

**SUNAN JAM'IYYA**

1) Sunan Jam'iyyar zai kasance "Youth Party", mai takaitaccen suna "YP".

**IKON KUDNDIN TSARIN MULKIN JAM'IYYA**

2) Tattare da tanade-tanaden kundin tsarin mulkin jamhuriyyar Nijeriya ta dokar zabe da qa'idoji da sharuddan hukumar INEC da sauran tanade-tanaden doka da suka jibinci haka, wannan kundin tsarin mulkin jam'iyyar, shi zai kasance madaukaki kuma tanade-tanadensa masu iko ne, a kan daukacin 'yan jam'iyyar

**TAKE DA KIRARIN JAM'IYYA**

3) Za a rinqa yi wa Jam'iyyar Taken " hadin Kai da Aiki tuquru don tabbatar da ci gaba" wato "UNITY, SERVICES AND DEVELOPMENT" kuma kirarin Jam'iyyar zai kasance ne "YP-Kyautata Gaba" a turance "YP-SHAPE THE FUTURE" tare da daga 'yan yatsan tsakiya dana manuniya wato dan yatsan kusa da babban yatsa na hannun dama a tare kuma a ware.

## TUTA DA TAMBARIN JAM'IYYA.

4) Tutar Jam'iyyar za ta kasance ne fara mai dauke da tambarin kore da ruwan kwai, Tambarin zai kasance ne mai alamar 'yan yatsun hannun dama biyu na tsakiya da manuniya a dage kuma a ware cikin kalolin kore da ruwan kwai.

## OFISHIN JAM'IYYAR MAI RIGISTA

5) Babban ofishin Jam'iyyar da aka yi wa rigista, zai kasance ne a babban birnin tarayya Abuja. Kuma za a samar wa babban ofishin Jam'iyyar rassa lokaci zuwa lokaci, da zaran ta amince da hakan.

## QA'IDOJIN JAM'IYYA

**6)**

1. Jam'iyyar za ta kasance ta demokaradiyya, kuma, za ta riqa tafiyar da manufofinta ba tare da nuna banbance-babance da son zuciya ba.
2. Shirye-shirye da manufofin Jam'iyyar, za su rinqa kasancewa ne ta la'akari da 'yan jam'iyya, kana shugabancin jam'iyyar shi ke da nauyin kula da 'yan jam'iyyar.
3. Jam'iyyar za ta yi qoqarin fadawa takarar neman kowanne muqamin zabe a Najeriya, kuma, da wannan manufa, jam'iyyar za ta duqa neman goyon bayan jama'a daga kowanne bangare.
4. Jam'iyyar, a fafutukar neman samun hadin kai don cimma wata manufa, wajibi ta mutunta harshe da al'adu da addinan 'ya'yanta mabanbanta.
5. Jam'iyyar, ba za ta lamunci duk wasu ayyukan nuna fifiko da siyasar batanci da raba kai ba, kuma za ta kasance mai haramta yin kalaman nuna wariyar kabilanci da batanci .
6. Jam'iyyar za ta rinqa goyon bayan shigar mata da naqassasu cikinta, ta hanyar basu damar yin wakilci a kowanne mataki.
7. Jam'iyyar za ta rinqa mutunta 'yanci da ra'ayoyin, da ba da damar musayar shawarwari da bayanai da basu shafi iko da martabar Jam'iyyar ba.
8. Daukacin muhimman qa'idojin Jam'iyyar za su riqa samun jagorancin dokoki da qudirorin qasa ne, kamar yadda suke qunshe a babi na 11 na kundin tsarin mulkin Jamhuriyyar Najeriya na shekarar 1999 da aka yi wa gyaran fuska.

**BABI NA BIYU**

SASHI NA XAYA

ZAMA XAN JAM'IYYA

7.

1. Qofar neman zama dan' jam'iyyar, za ta kasance ne a bude ga daukacin 'yan Najeriya, da shekarunsu ya kai goma sha takwas (18), musamman ga wadanda suka amince da manufofi da qudurorin jam'iyyar, kuma cancantar zama dan jam'iyyar ba ruwanshi da jinsin da mutun ya fito ko yanayin haihuwa da tsatsonsa ko addinin mutum ko ma duk wani matsayi na ma'aikaci ko ba ma'aikaci ba a gwamanatocin tarayya da jihohi da qananan hukumomi.
2. Rigistar dan' jam'iyya za a ajiye ta ne a matakin ofishin gunduma na jam'iyyar, amma daukacin jadawalin bayanai 'ya'yan jam'iyyar da suka yi rgista zai kasance ne a shalkwatar jam'iyyar da ke Abuja.
3. Kuma wajibi rigistan zama dan' Jam'iyyar na matakin gundumomi ta samu sahannun shugaba da sakataren ofishin Jam'iyyar na gundumar don zama sahihiya.
4. Mai son zama cikakken dan' Jam'iyya sai Ta/ya yi..
   a) Rigistar da Jam'iyyar a gundumarta/sa ko inda ta/yake da zama ko gudanar da aiki na dindindin; tare da
   b) Biyan duk kudaden yin rigistar da ake buqata kafin zama dan' jam'iyyar.
5. Kwamitin zattarwar Jam'iyya na gunduma, shi ke da ikon duba takardun neman zama dan Jam'iyyar, da amincewa ko qin amincewa da duk wata takardar neman zama dan' Jam'iyyar.
6. Uwar Jam'iyya na iya qin amincewa da duk wata takardar neman zama dan' Jam'iyya bisa wadannan dalilai da ke biye a qasa.
   a) Rashin sahihancin bayanai da rashin shedar da'a da sauran dabi'u da suka ci karo da manufofi da qudirorn Jam'iyyar; ko
   b) Ana tunanin mai neman zama dan Jam'iyyar zai iya haddasa rikici a Jam'iyyar; ko
   c) Mai neman zama dan' Jam'iyyar, dan' wata Jam'iyya ce a Najeriya;
7. Kudin ya tanadar da cewa, duk wani batun qin amincewa, sai uwar Jam'iyyar ta yi bita a kan shi.
8. Za a iya soke katin zama dan' Jam'iyyar bisa wadannan laifuka da aka kama dan Jamiyyar da aikatawa, ga su kamar haka:
   a. Bayanan qarya da rashin da'a ga manufofi da qudurorin Jam'iyyar;
   b. Yin dabi'un da suka haifar da rikici da rudani ga Jam'iyyar; da
   c. Tsayawa zabe ko neman takaradar zama wakilin zabe (Agent) na wani dan' takaran Jam'iyya da ke hamaya da dan' takaran Jam'iyyar Youth Party;
   d. Shiga ko mara bayan wata Jam'iyya da ba Jam'iyyar Youth Party ba, ko fifita duk wani dan takara a kan dan takaran Jam'iyyar Youth Party, fitowa takara da yin

adawa da dan' takarar Jam'iyyar Youth Party, yin hakan shi zai haifar da rashin cancantar zama dan Jam'iyyar kai tsaye

e. Nema da amincewa da muqaman siyasa na gwamnatin wata Jam'iyya; sannan kuma
f. Ba za a soke katin zama dan' Jamiyyar ba, sai an sanar da dan' Jam'iyyar laifukan da suka sanya a soke katin nasa tare da bashi isasshiyar damar bada amsa. Inda a sakin layi na daya (C) na kundin, ya tanadar da cewa; nan take za a dakatar da dan' Jam'iyyar kuma a yanayi na gaggawa, uwar jam'iyyar ce da ke da cikakken iko, za ta dakatar da dan' Jam'iyyar kafin kamala la'akari da batun soke katin dan' Jam'iyyar.

9. Za a miqa katin zama dan' Jam'iyya ne ga wanda ya yi rigista da Jam'iyyar, kuma zai kasance ne dauke da hotan dan' Jam'iyya.
10. Shalkwatar Jam'iyyar ta qasa ce za ta samar da katin zama dan; Jam'iyyar kuma shugaba da Sakataren Jam'iyyar na qasa su tabbatar da sahihancin sa ta hanyar rattaba hannunsu.

**<u>MATAKAN SAKE ZAMA DAN JAM'IYYA</u>**

**<u>8.</u>**

1) Mutumin da ke da sha'awar komowa Jam'iyya bayan ya barta, ga abin da zai yi kamar haka:
    a. Miqa takardar neman zama dan' jam'iyyar ga sakataren Jam'iyyar na gundumarta/sa don sake komowa dan' Jam'iyyar.
    b. Amma idan har kwamitin zattarwar Jam'iyya na qasa, ya dakatar da dan' Jam'iyyar, to shi ne fa sai an yi bincike a kan hakan tsawon qasa da shekara daya, kafin maido ta/ shi a matsayin dan' Jam'iyya.
2) Bisa tanadin kundin, shashi na 8(i)(a), ya nunar cewa dan' Jam'iyya da ake bincikesa, na da 'yancin halartar kowanne taron Jam'iyyar, amma kuma bai da 'yancin kada quri'ar amincewa da wani batu a wurin tarukan, kuma, ba zai fito neman muqamin siyasa qarqashin tutar Jam'iyyar ba.
3) 'Ya'yan Jam'iyyar za su rinqa biyan kudaden harajin da Jam'iyyar ta sanya a matakan gunduma, kuma wajibi ne, alamta shi a katin zama dan' Jam'iyyar, kuma, duk dan Jam'iyya da ya gaza biyan harajin sa, har na tsawon shekara biyu, to, babu shakka, ba zai mori 'yanci da dama na dan' Jam'iyya ba, wannan tanadin kundin, ya kuma tanadar da cewa kwamitin zattarwar Jam'iyyar ne ke da Daman bullo da hukuncin da ya kamanci dan' Jam'iyya da karya dokar biyan kudaden harajin Jam'iyyar da sanya kudaden harajin masu sauqin biya.
4) Za a dore amfani da tsarin yin rigistar katin zama dan' jam'iyyar ce, ta na'urar zamani don tabbatar da tsaro da kaucewa aikata ba daidai ba, kuma, daukacin cibiyoyin yin rigistan zama dan' jam'iyyar na daukacin gundumomi, za a rufe sune kwanaki talatin (30) kafin manyan tarukan Jam'iyyar.

5) Za a inganta tsarin adana bayanan 'ya'yan Jam'iyyar, don samun tsarin ajiyewa da adana bayanai na bai daya a daukacin matakan Jam'iyyar.
6) 'Ya'yan Jam'iyyar, wajibi ne, su tabbatar da ganin sun tantance sunansu kafin rufe yin rigistar, kuma shugabanni da sakatarorin gunduma na Jam'iyyar ne ke da alhakin tabbatar da shahihancin bayanan, kafin tsarin tafiyar da batun miqa suna, ya soma.
7) Bayanan daukacin masu katin zama yan' Jam'iyyar masu rigista, za su kasance ne bayanan sirri na Jam'iyya.

**BACEWA KO RASHIN KATIN ZAMA DAN JAM'IYYA**

**9**

1) Sashi na 8(3) na kundin tsarin mulkin Jam'iyyar ya tanadar da cewa, duk dan' Jam'iyyar da ya gaza sabunta katin dan' Jam'iyyarsa ta hanyar qin biyan harajin da Jam'iyya ta sanya na sabunta katin duk shekara, har tsawon shekaru biyu bayan wannan wa'adin, zai rasa samun 'yanci da dama a matsayinsa na dan' Jam'iyya, in kuma ya kai shekara uku zuwa sama, za a dakatar da shi daga zama dan' Jam'iyyar.
2) Duk dan' Jam'iyyar da ya rasa katinsa na zama dan' jam'iyyar bisa dalilin rashin biyan duk wani harajinsa na jam'iyya ko ya gaza cimma wata qa'idar biyan kudi da ke kansa, ba zai komo Jam'iyyar ba, har sai ya biya daukacin bashin harajin da ake binsa bashi tare da hukunce-hukunce.
3) Bugu da qari, duk dan' jam'iyyar da ya rasa katin zama dan' jam'iyyar bisa dalilan da basu wuce rashin biyan kudaden sabunta katin jam'iyya na shekara-shekara ba, za a iya maido da shi matsayin dan jam'iyyar ne idan har kwamitin zattarwar jam'iyyar na mazabarsa ya miqa takardar shedar yabo, ta hannun kwamitin zattarwar jam'iyyar na qaramar hukuma ga kwamitin zattarwar jam'iyyar reshen Jiha da kwamitin ayyuka na qasa don samun amincewar kwamitin zattarwar jam'iyyar na qasa.

**MATSAYIN 'YA'YAN JAM'IYYAR DA SUKA KOMO JAM'IYYAR BAYAN SUN SAUYA SHEKA ZUWA WATA JAM'IYYA.**

10. Duk dan' jam'iyya da ya sauya sheka daga Jam'iyyar zuwa wata Jam'iyya, amma daga bisani ya yanke shawarar komowa Jam'iyyar ta Youth Party, zai rasa matsayinsa da damar da yake da ita a matsayinsa na jigo tun lokacin da yake Jam'iyyar tun da farko.

**SASHE NA BIYU**

RASSAN JAM'IYYA NA QASASHEN WAJE

11

1) Bisa amincewar kwamitin zattarwar jam'iyya na qasa, 'ya'yan jam'iyyar da ke da zama a qasashen waje masu huldar diplomasiyya, qasa da hamsin ne (50), za su iya

kafa reshen jam'iyyar a qasar da suke da zama, amma sai dai basu cancanci amfana da duk wani 'yanci zama yan' jam'iyyar ba, tun da yake ba su yi rigistar zama 'ya'yan jam'iyya ba a gundumominsu daban-daban da ke Nijeriya ba.

2) Domin cim ma manufar tafiyar da ayyukan rassan Jam'iyyar na qasashen waje, za a samar da wasu manyan jami'ai a ofishin sakataren Jam'iyyar na kasa wadanda za su rinqa tafiyar da ayyukan.

## RASSAN JAM'IYYAR NA DALIBAI

12

1) Bisa amincewar kwamitin zattarwar Jam'iyya na qasa, 'ya'yan jam'iyyar dalibai da ke karatu a manyan makarantun da aka amince dasu, da basu kai qasa da adadi hamsin ba, zasu iya kafa reshen Jam'iyyar a makarantunsu daban-daban, amma kuma ba za su cancanci amfana da daukacin 'yancin zama yan' jam'iyya ba, domin basu yi rigistar zama yan' jam'iyyar ba a gundumominsu daban-daban da ke Nijeriya da cim ma sauran qa'idoji ba.
2) Don tafiyar da ayyukan rassan jam'iyya na daliban yadda ya kamata, za a samar da shugabannin rassan daliban manyan makarantun daban-daban. Ta (SYP).

## RASSAN JAM’IYYAR NA KASUWANNI

13

1) Bisa amincewar kwamitin zattarwar jam’iyyar na qasa, ‘ya’yan jam’iyyar ‘yan kasuwa da basu gaza adadi hamsin (50) ba, za su iya kafa reshen jam’iyyar na ‘yan kasuwa a kasuwannin da suke gudanar da kasuwancinsu, amma kuma za su amfana da cikakken ‘yancin zama yan’ jam’iyyar ne, in suka yi rigista a mazabunsu daban-daban a Nijeriya da cike daukacin sauran qa’idojin jam’iyyar.
2) Rassan jam’iyyar na kasuwanni za a daganta su ne da gunduma mafi kusa da kowacce kasuwa, kuma tana da ‘yancin miqa shugaba na reshen jam’iyyar daga bangaren zattarwar jam’iyyar na gunduma, kuma, wannan muqami sauran shugabannin kasuwanni na da damar fitowa takarar neman kujerar, idan aka sami kasuwa a gunduma daya, zaben zai kasance ne bisa tsarin gamayya na wakilan zaben.
3) Za a samar da wasu manyan jami’ai da za su rinqa tafiyar da harkokin rassan jam’iyyar na kasuwanni daga ofishin sakatarorin jam’iyyar na qasa.

## RASSAN JAMIYYAR NA MANOMA

14

1) Bisa amincewar kwamitin zattaswar jam’iyyar na qasa za a bai wa manoma da ke da rigista da jam’iyyar damar kafa rassan jam’iyyar Youth party a bangarorin nomansu daban-daban.
2) Za a samar da wasu jami’an da za su rinqa tafiyar da rassan jam’iyyar na manoma daga ofishin sakataren jam’iyyar na qasa.
3) Neman kafa rassan manoma na jam’iyyar zai kasance ne bisa wadannan qa’idoji:
    a. ‘ya’yan rassan qasa da mutane hamsin .
    b. Samar da wani shugaba mai kwazo da sadaukar da kai.
4) Za a samar da duk qa’idoji da sharuddan rassan manoman jam’iyyar ne, a shafin sadarwa na jam’iyyar wato website.
5) . (5) Bisa amincewa, duk wani reshen manoma na jam’iyyar zai kasance ne:
    a. Jingine da gundumar da akasarin ‘ya’yansa suka yi rigista; kuma
    b. Yana da ‘yancin miqa sunan shubagan manoma ga kwamitin zattaswar gunduma na jam’iyyar, a inda aka samu rassan manoman jam’iyyar fiye da daya a gunduma, kuma shugaban rassan na da damar neman zama dan kwamitin zattaswar jam’iyyar na gunduma. Za a nemi muqamin ne ta hanyar gudanar da zabe, inda kowanne reshen manoma na jam’iyyar zai gabatar da wakilan zabensa daidai da wakilansa.

RASSAN JAM'IYYAR NA QUNGIYAR MA'AIKATA

15

(1) Bisa amincewar shugabannin jam'iyyar na qasa, za a ba da dama ga 'ya'yan jam'iyyar da ke da rigista wadanda suke a matsayin 'ya'yan qungiyar ma'aikata, su kafa qungiyar ma'aikata reshen jam'iyyar Youth Party a qungiyoyinsu daban-daban.
(2) Za a samar da wasu jami'ai da za su rinqa tafiyar da harkokin rassan qungiyar ma'aikatan jam'iyyar daga ofishin sakataren jam'iyyar na qasa.
(3) Neman kafa reshen jam'iyyar na qungiyar ma'aikatan, zai kasance ne bisa wadannan qa'idoji;
    a. 'Ya'yan reshen, qasa da mutane hamsin (50) ;
    b. Samar da shugaba mai kwazo da sadaukar da kai.
(4) Cikakkun qa'idoji na reshen qungiyar ma'aikatan jam'iyyar, za su kasance ne a shafin yanar gizo.
(5) Bisa amincewar sharadi, duk wani reshen jam'iyyar na ma'aikata zai kasance ne:
    a. Jingine da gundumar da akasarin wakilansa suka yi rigista; kuma
    b. Yana da 'yancin miqa shugaban ma'aikatan jam'iyyar ga kwamitin zattaswar gunduma, a inda aka samu sassan jam'iyyar na qungiyar ma'aikatan daban-daban, don damar da yake da ita na zama dan kwamitin zattaswar jam'iyyar na gunduma, amma sai dai hakan zai kasance ne ta hanyar zabe bisa daidaiton wakilan zabensa na gunduma.

**BABI NA UKU**

**SASHI NA DAYA**

**ABUBUWAN KIYAYEWA DA XA'A**

16

1. Dan jam'iyya zai kasance:
   a) Mai shiga cikin ayyukan Jam'iyya a gundumarsa;
   b) Daukar duk matakana da suka wajaba na fahimta da yadawa da aiwatar da manufofi da qudirori Jam'iyyar; da
   c) Yin qoqarin jurewa yanayin walwala da al'adu da siyasa da matsalolin tattalin arziqin qasa.
   d) Yaqi da duk wata furofaganda da ke da illa ga Jam'iyyar da kare manufofi da shirye-shiryen Jam'iyyar;
   e) Yin hamayya ga duk yunqurin haifar da rashin jituwa da wariyar qabilanci da addini da siyasa;
   f) Kasancewa mai da'a da riqon gaskiya da amana da biyya ga matakan mafiya rinjaye da shugabancin Jam'iyyar; da
   g) Kaucewa dab'ar bugawa da raba duk wata takardar da ke qunshe da ayyuka da manufofin jam'iyyar ba tare da izini ba;
   h) Dan jam'iyya ya tabbatar ya yi rigistar kada quri'a a mazabar da yake da zama; da
   i) Biyan kudaden haraji da sauran kudaden da za a rinqa buqata lokaci zuwa lokaci wanda Babban taron da shugabancin Jam'iyyar suka amince a biya;
   j) Wannan kundin tsari ya tanadar da cewa sai kin/ka cancanci kada quri'a sannan za a zabe ki/ka a tarukan Jam'iyyar ko a zabuka;
   k) Kasancewa mai biyayya ga jam'iyyar tare da kaucewa yin duk wani abu da zai sabawa tanadin kundin tsarin mulkin jam'iyya;
2. Ba a yadda wani dan jam'iyyar na kowanne mataki ba ya rinqa fallasa matakan zattarwa na jam'iyyar sai da izini.
3. Daukacin jami'an gwamnati da aka zaba ko aka nada qarqashin inuwar jam'iyar,. Za su kasance ne masu biyayya ga qa'idojin Jam'iyyar.
4. Babu wani dan' jam'iyyar da aka yarda ya sanar da jama'a irin rashin jituwa da rikici da ka'iya wanzuwa a jam'iyyar, sai da izini . Don warware matsalar.
5. Babu wani dan' jam'iyyar da ke da hurumin sukar manufofi kowacce gwamnati da aka zava qarqashin tutar Jam'iyyar a bainar jama'a sai idan har an take tanadin shawo qorafe-qorafen bangaren da ya fusata bayan bin wannan matakai kamar haka:
   a) A gabatar da wani qorafi da ra'ayoyi da shawarwari ga jam'iyyar don daukar mataki da ya kamata a cikin wata daya;

b) Rashin gamsuwa da duk wani matakin jam'iyyar daga majalisar dattawan jam'iyyar;
c) Duk wani rashin gamsuwa da matakan jam'iyya da majalisar dattawan jam'iyyar daga kwamitin amintattu na jam'iyyar.

6. Babu wani dan' jam'iyya da zai hada gwiwa da wasu jam'iyyu ko qungiyoyi don haifar da naqasu ga jam'iyyar da duk wata gwamnati da aka zaba qarqashinta.
7. Babu wani dan' jam'iyya da zai karbi nadin muqamin siyasa na wata gwamnatin jam'iyyar siyasa.

## SASHI NA BIYU

## WAJIBABBUN NAUYIN DA YA RATAYA A WUYAN JAM'IYYAR DA 'YAN'YANTA

17

1) Wajibi ne jam'iyyar ta rinqa samar da gurabun ayyuka ga 'ya'yanta; da daukar matakan qarfafa gwiwar ayyukan sa kai.
2) Jam'iyyar za ta rinqa samar da sahihan matakai da nufin qarfafa kwarin gwiwar 'ya'yanta, ta hanyar aikace-aikace ka'in da na'in da ke da nufin inganta kyakkyawar fahimta a tsakanin 'ya'yanta.
3) Jam'iyyar ce za ta rinqa samar da ingantaccen tubalin kare 'ya'yanta na kundin tsarin mulki na damar yin zabe tare da tabbatar da samun nasarar duk wani dan' jam'iyyar da ya tsaya takarar kowanne irin zave qarqashin tutar jam'iyyar.
4) Jam'iyya ce za ta rinqa kare muradun daukacin 'ya'yanta a ko da yaushe kuma ba za ta dauki wani matakin yin duk wani abu ba da ka'iya shafar martaba ko yin illa ga 'ya'yanta.

**BABI NA HUDU**

**TSARIN MULKI NA JAM'IYYA**

**SASHI NA DAYA**

18

1) Tsarin tafiyar da jam'iyyar, zai kasance ne a wadannan matakai da ke biye:
   a) Gunduma;
   b) Yankin qaramar hukuma (LG)
   c) Jiha; da matakin
   d) Qasa.
2) Don cim ma manufar zabuka, za a samar da wani sashi na wayar da kan masu kada quri'a da zai yi aiki a bangarori kamar haka:
   a) Mazabar xan majalisar dokokin jiha;
   b) Mazabar tarayya; da
   c) Mazabar xan majalisar magabata.
3) Za a samar da sakatariyar jam'iyyar a kowanne mataki na jam'iyya.
4) Game da manufar tsarin tafiyar da jam'iyyar, babban birnin tarayya Abuja ne zai kasance cibiyar tafiyarwa.

**SASHE NA BIYU**

**SASSAN TAFIYAR DA TSARIN JAM'IYYA**

19

1) SASSAN TAFIYAR DA TSARN JAM'IYYAR ZAI QUNSHI:
   a) Taron Gunduma;
   b) Kwamitin zattarwa na gunduma
   c) Taron karamar hukuma;
   d) Kwamitin zattarwa na qaramar hukuma;
   e) Jiga-jigan jam'iyya na qaramar hukuma;
   f) Taron jiha;
   g) Kwamitin zattarwa na jiha
   h) Majalisar dattawa ta jiha;
   i) Jiga-jigan jiha;
   j) Qusoshin majalisar magabata;
   k) Babban taron jam'iyyar na qasa;
   l) Kwamitin zattarwa na qasa; da

m) Jiga-jigan jam'iyya na qasa.

2) Shawarwari a dukkan matakan jam'iyyar, za su kasance ne daidai da bin qaidojin demokaradiyya na mutum daya quri'a daya. A inda duk aka sami dambarwa a kan haka, shugaba ne zai jefa quri'a daya.

**<u>SASHE NA UKU</u>**

**<u>MATAKIN GUNDUMA</u>**

**<u>TARON GUNDUMA NA JAM'IYYA</u>**

SASSAN TAFIYAR DA TSARIN JAM'IYYA

20

1) Taron jam'iyyar na gunduma, zai qunshi daukacin 'ya'yan jam'iyyar da ke da rigista a gundumar.

<u>AYYUKAN BABBAN TARO</u>

2) Ayyukan taron jam'iyyar na gunduma zai kasance ne:
   a) Karbar rahotannin jami'an gunduma;
   b) Karbar rahotannin masu binciken kudi;
   c) Amincewa da kasafin kudin gunduma;
   d) Zaven wakilan kwamitin zattarwa na gunduma;
   e) Zaven wakilan taron jam'iyya na qaramar hukuma da jiha;
   f) Gudanar da zavukan muqaman fidda dan takaran da ke neman zaben muqaman gwanati; da
   g) Tafiyar da sauran irin wadannan ayyuka na kare muradun jam'iyya kamar yadda jiga-jigan uwa jam'iyyar suka amince a yi.

<u>TARUKA</u>

3) Shugaban kwamintin zattarwa na gunduma zai kasance mai kiran taron gunduma a kalla sau daya a kowanne watannin uku na shekara.
4) Adadin 'ya'yan jam'iyyar a taron gunduma za su kasance ne xaya bisa uku kuma bangaren masu rinjaye ne zai iya gabatar da duk wani qudiri.
5) Za a gudanar da wani taron gunduma na musamman idan kashi biyu bisa uku na taron 'ya'yan jam'iyyar gundumar suka nemi a yi kuma taron zai gudana ne cikin mako guda da neman buqatar yin taron.

## KWAMITIN ZATTARWA NA GUNDUMA

21

1) Zai zamana akwai kwamitin zattarwa na gunduma mai qunshe da:
    a) Shugaba;
    b) Mataimakin Shugaba;
    c) Sakatare;
    d) Mataimakin sakatare;
    e) Da mai bada shawara kan harkokin shari'a na gunduma, wanda zai kasance lauya ne.
    f) Sakataren yada labarai;
    g) Mataimakin mai yada labarai
    h) Ma'aji
    i) Mataimakin ma'aji;
    j) sakataren shirye-shirye;
    k) mataimakin sakataren shirye-shirye; da
    l) mai binciken kudi; da sakataren kudi; da
    m) shugaban daliban jam'iyyar Youth Party (SYP);
    n) shugaban manoma
    o) shugaban 'yan kasuwa; da
    p) zaben wakilai biyar a taron gunduma, da kalla mata biyu daga cikinsu a inda ake bukata.

AYYUKA

2) Ayyukan kwamitin zattarwa na gunduma za su kasance ne:-
    a) Tafiyar da harkoki a matakin gunduma;
    b) Samar da kudade ga jam'iyya;
    c) Neman 'ya'yan ga jam'iyya;
    d) Tsara dabarun gudanar da gangamin siyasa;
    e) Neman wa jam'iyyar masu kada quri'a ta hanyar wayar da kai;
    f) Aiwatar da shawarwarin taron gunduma da na sauran jiga-jigan bangarorin tafiyar da tsarin jam'iyyar;
    g) Karbar rahotan mai binciken kudi; da
    h) Gudanar da sauran ayyukan da za su kare muradun jamiyyar da za a buqaci kwamitin lokaci zuwa lokacci.

TARUKA

3) Kwamitin zattarwar jam'iyyar na gundumaa zai rinqa ganawa ne sau daya a wata.

4) Shugaban gunduma ne zai kasance mai kiran tarukan kwamitin zattarwa na gunduma.
5) Za a gudanar da wani kwarya-kwaryan taron kwamitin zattarwa na gunduma, idan kashi biyu bisa uku na wakilan kwamitin zattarwar jam’iyyar na gunduma ko kashi daya bisa uku na ‘ya’yan jam’iyyar da ke da rigista a gundumar suka buqaci yin hakan kuma wannan taron zai kasance ne cikin kwanaki bakwai da neman bukatar yin taron.
6) Adadin wakilan da zasu halarci taron kwamitin zattarwa na gunduma, za su kasance ne daya bisa uku na ‘ya’yan jam’iyyar kuma bangaren da ya yake da rinjaye ne zai rinqa gabatar da duk wani qudiri taron.

**SASHI NA HUDU**

**BABBAN TARON JAM’IYYAR NA YANKIN QARAMAR HUKUMA**

SASSAN TAFIYAR DA TSARI

22

1) Zai kasance akwai wani yankin qaramar hukuma wanda zai qunshi:
    a. Shugaban jam’iyyar qaramar hukuma da sauran wakilan kwamitin zattarwa na qaramar hukumar; da
    b. Zababben shugaban qaramar hukuma da mataimakin shugaba da kansiloli wadanda suka kasance a matsayin ‘ya’yan jam’iyyar;
    c. Daukacin shugabanni da sakatarorin kwamintin zattarwa na gundumomin da suka fito daga yankin qaramar hukumar;
    d. Wakilai uku daga kowacce gundumar qaramar hukuma da aka zava a taron gunduma, a qalla a samu mace daya daga cikin adadin, wanda dukkansu za a sanar da su ayyukan da za su yi bayan kamala taron;
    e. Shugaba da sakataren jam’iyyar a qaramar hukumar.

AYYUKA

2) Ayyukan taron jam’iyyar na qaramar hukuma za su kasance ne:-
    a. Zaben wakilan kwamitin zattarwar Jam’iyyar na qaramar hukumar;
    b. Zaben wakilan babban taron jam’iyyar na qasa dana zabe na qaramar hukuma;
    c. Amincewa da kasafin kudin jam’iyyar a matakin qaramar hukuma; da
    d. Karbar rahotan mai binciken kudin qaramar hukumar.

TARUKA

3) Tarukan jam’iyyar na qaramar hukuma zai kasance mai gudana ne, qasa da sau daya a shekara.
4) Shugaban kwamitin zattarwa na jiha, shi zai kasance mai kiran tarukan yankin qaramar hukuma.
   Za a gudanar da wani kwarya-kwaryar taron yankin qaramar hukuma na musamman ne, idan aqalla biyu bisa uku na shugabannin gundumonin yankin qaramar hukumar suka nemi buqatar yin haka.
5) Adadin wakilan zabe na taron qaramar hukuma za su kasance ne xaya bisa uku, kana a sami halarcin daukacin gundumoni na qaramar hukuma, qasa da biyu bisa uku, kuma wani bangaren mafiya rinjaye ne zai kasance mai zattas da duk wani qudiri.

## KWAMITIN ZATTASWA NA YANKIN QARAMAR HUKUMA

SASSAN TAFIYAR DA TSARE-TSARE.

23

1) Zai zamana akwai kwamitin zattaswa na qaramar hukuma, wanda zai qunshi :-
   a. Shugaba;
   b. Mataimakin shugaba;
   c. Sakatare;
   d. Mataimakin sakatare;
   e. Mai ba da shawara kan shara'a na jam'iyya wanda zai kasance lauya;
   f. Mataimakin mai baiwa jam'iyya shawara kan harkokin shara'a;
   g. Sakataren yada labarai;
   h. Mataimakin sakataren yada labarai;
   i. Ma'aji;
   j. Mataimakin ma'aji
   k. Sakataren shirye-shirye;
   l. Mataimakin sakataren shirye-shirye;
   m. Mai binciken kudi;
   n. Mataimakin mai binciken kudi;
   o. Sakataren kudi;
   p. Mataimakin sakataren kudi;
   q. Shugaban Daliban Jam'iyyar Youth party (SYP);
   r. Shugaban manoma;
   s. Daukacin shugabannin gunduma; da
   t. Sauran tsoffin wakilai shida, aqalla mata biyu.

AYYUKA

2) Ayyukan kwamitin zattarwa na qaramar hukuma za su kasance ne kamar haka:-
   a. Ganowa da warware batutuwan siyasa da walwala da tattalin arziki da za su haifar da damuwa ga yankin qaramar hukuma;
   b. Karva da aiwatar da rahotannin da suka fito daga gundumomi kan batun
      i. Zama yan' jam'iyya
      ii. Asusun tara kudade
      iii. Tsara dabarun samun nasarar gangamin siyasa da zabe; da
      iv. Wayar da kan masu kada quri'a
   c. Samar da dabarun tabbatar da ingantaccen tsarin sadarwa tsakanin gundumomi da yankin qaramar hukuma;
   d. Daukar nauyin tafiyar da harkokin mulkin jam'iyyar a yankin qaramar hukuma
   e. Aiwatarwa da shawarwarin taron qaramar hukuma da sauran na jiha; da

f. Daukar sakatarori a daukacin rassan qaramar hukuma na jam'iyya.

TARUKA

3) Kwanitin zattarwar jam'iyya na qaramar hukuma zai gudana ne qasa da lokuta biyar a wata.
4) Shugaba ne zai kasance mai kiran tarukan.
5) Taro na musamman na kwamitin zattarwar jam'iyya na qaramar hukuma zai gudana ne, idan har biyu bisa uku na wakilan kwamitin zattarwa na qaramar hukumar suka buqaci hakan kuma irin wannan taron zai kasance ne cikin kwanaki bakwai da neman buqatar.
6) Adadin wakilan kwamitin zattarwa na qaramar hukumar za su kasance ne daya bisa uku da aka janyo daga aqalla gundumomin yankin qaramar hukumar biyu bisa uku, kuma bangaren mafiya rinjaye ne zai zattas da qudiri.

## JIGA-JIGAN JAM'IYYA NA QARAMAR HUKUMA

24

1) Zai kasance akwai jiga-jigan jam'iyya na yankin qaramar hukuma a kowacce majalisar qaramar hukuma na tarayya za su qunshi wakilai kamar haka:-
   a. Shugaban jam'iyya na yankin qaramar hukuma, wanda zai kasance a matsayin shugaba;
   b. Shugaba da sakatare da ma'aji da shugaban manoma da na 'ya kasuwa da na daliban jam'iyyar Yoth Party.
   c. Wakilan zattarwa na qasa da jiha da na shiyya da majalisar magabata na jam'iyyar daga yankin qaramar hukuma;
   d. Wakilan majalisar dokoki na jam'iyyar daga yankin qaramar hukuma;
   e. Wakilan kwamitin amintattu daga yankin qaramar hukuma;
   f. Masu riqe da muqaman siyasa daga yankin qaramar hukuma;
   g. Daukacin tsaffin wakilan majalisan dokoki da suka fito daga shiyyar gundumar dan' majalisar magabata wadanda ke cikin jam'iyyar;
   h. Shugaba da mataimakin shugaba da sakatare na yankin qaramar hukuma da kansilolin kula da sassa uku da shugaba ya zava, wadanda ke jam'iyya; da
   i. Dattawa biyar na jam'iyya a qaramar hukuma da jiga-jigan jam'iyya suka zava.

AYYAUKA

2) Jiga-jigan jam'iyya na yankin qaramar hukuma za su kasance ne masu daukar matakan gaggawa ne akan muhimman batutuwa da ke shafar siyasa da tattalin arziqin yankin qaramar hukuma ko jiha. Kuma matakansu za su kasance ne ba da shawarwari da samar da hanya mafita ga yadda za a tafiyar da matakan kwamitin zattarwa.

TARUKA

3) Jiga-jigan jam'iyya na qaramar hukuma za su gana ne qasa da sau biyu a shekara.
4) Taro na musamman na jiga-jigan jam'iyya na qaramar hukuma zai gudana ne idan adadin 'ya'yan jam'iyyar da ke buqatar hakan sun kai biyu bisa uku kuma za a gudanar da taron ne a cikin kwanaki bakwai da neman buqatar yin hakan daga wakilan jam'iyya
5) Adadin jiga-jigan jam'iyyar na qaramar hukumar za su kasance ne daya bisa uku kuma bangaren mafiya rinjaye ne sasu zattas da duk wani qudiri.

**SASHI NA BIYAR**

Taron Jam'iyya na jiha

Tsari da bangarorin tafiyar da taron

25

1) Zai kasance akwai taron jam'iyya wanda zai qunshi:
   a. Shugaba na jiha, wanda zai kasance shugaba;
   b. Wakilan kwamitin zattarwa na jiha;
   c. Gwamna da mataimakin Gwamna na jiha, muddin in sun kasance wakilan jam'iyyar;
   d. Wakilan majalisar dattawa na jiha a jam'iyyar
   e. Dan takarar Gwamna na Jam'iyyar;
   f. Wakilan majalisar dokoki na jiha kuma 'ya'yan jam'iyya;
   g. Daukacin zavavvun shugabannin majalisun kananan hukumomi da mataimakansu na jam'iyyar;
   h. Daukacin sakatarori da ma'aji-ma'ajin jam'iyyar na qaramar hukuma;
   i. Daukacin shugabannin 'yan kasuwa da manoma da na bangaren daliban jam'iyyar na qaramar hukuma;
   j. Wakilan zabe uku-uku daga kowacce gunduma da aka zaba a tarukan gunduma aqalla mace daya daga cikin su, kuma dikkansu za su gudanar da ayyukan da ya sa aka zabe su bayan kamala tarukan;
   k. Tsoffin wakilan kwamitin zattarwa na jiha da basu bar ba;
   l. Tsoffin Gwamnoni da mataimakan Gwmnoni najam'iyyar da suke a jam'iyyar.
   m. Tsoffin shugabannin majalisar dokokin jiha da mataimakansu, da basu bar jam'iyyar ba;
   n. Tsoffin wakilan dokokin jiha waxanda ke ci gaba da kasancewa a matsayin 'ya'yan jam'iyyar.

AYYUKA

2) Ayyukan babban taron jam'iyyar na jiha zai kasance ne:
   a. Amincewa da kasafin kudin rassan jam'iyyar na jiha.
   b. Zabar jam'ian kwamitin zattarwa na jiha
   c. Karbar rahotanni daga jami'an jam'iyyar da
   d. Karbar rahotan mai binciken kudi.

TARUKA

3) Babban taron jam'iyya na jiha zai kasance ne sau daya a kowacce shekara kuma kwamitin zattarwa na jiha shi zai tanadar da ran a da wurin da taron zai gudana, sannan taron zai gudana ne kafin gudanar da babba taron qasa.
4) Adadin 'ya'yan jam'iyyar da suka fito daga gundumoni dana majalisar magabata uku, biyu bisa uku ne ake sa ran za su kasance a wajen babban taron jam'iyyar na jiha, kuma bangaren mafiya rinjaye ne za su gabatar da duk wani qudiri.

## KWAMITIN ZATTARWA NA JIHA

26

1) Zai zamana a kwai wani kwamitin zattarwa na jiha da zai qunshi
    a. Shugaban jiha
    b. Da mataimakin shugaba na jiha
    c. Sakatare na jiha
    d. Mataimakin sakatare na jiha;
    e. Mai bai wa jam'iyya shawara kan harkokin shara'a na jiha kuma lauya;
    f. Mataimakin mai ba da shwara kan harkokin shara'a na jam'iyyar na jiha
    g. Sakataren yada labarai na jiha;
    h. Mataimakin sakataren yada labarai na jiha;
    i. Ma'aji na jiha;
    j. Mataimakin ma'aji na jiha
    k. Sakataren shirye-shirye na jiha;
    l. Mataimakin sakataren shirye-shirye na jiha;
    m. Mai binciken kudi na jiha;
    n. Mataimakin mai binciken kudi na jiha;
    o. Sakataren kudi na jiha;
    p. Mataimakin sakataren kudi na jiha;
    q. Shugaban manoma na jiha;
    r. Shugaban daliban Youth Party (SYP) na jiha;
    s. Shugaban 'yan kasuwa na jiha.

AYYUKAN KWAMITIN ZATTARWA NA JIHA

2) Kwamitin zattarwar jam'iyyar na jiha za kasance ne mai tafiyar da ayyukan da suka hada da:
    a. Tafiyar da harkokin mulkin jam'iyyar nayau da kullun na jam'iyyar a jiha kana shi ne ke da alhakin shirya babban taron jiha; da
    b. Ganowa da warware batutuwan siyasa da walwala da tattalin arziqin da ka'iya zama abin damuwa ga jam'iyyar a jiha;

c. Tafiyar da daukacin harkokin mulkin jam'iyyar a jiha da aiwatar da shawarwarin babban taron jiha, da umurnin kwamitin zattarwa na qasa da babban taron jam'iyyar; da
d. Shirya kasafin kudin shekara-shekara na reshen jam'iyyar na jiha.

3) Kwamitin zattarwana jiha zai rinqa ganawa ne qasa da sau biyu a wata tare da shugaban sa.
4) Kwamitin zattarwa na jiha zai gudanar da taro na musamman ne idan wakilan kwamitin biyu bisa uku suka bukaci hakan kuma taron zai kasance ne cikin kwanaki bakwai da neman buqatar hakan.
5) Kuma adadin wakilan kwamitin na jiha da ake sa ran su halarci taro za su kasance ne daya bisa uku, uku daga kowacce gundumar dan' majalisar magabata na jiha kuma bangaren mafiya rinjaye ne zai zattas da duk wani qudiri.

JIGA-JIGAN JAM'IYYA NA JIHA

27

1) Zai kasance akwai jiga- jigan jam'iyyar kowacce jiha ta tarayyar qasar nan, wannan rukuni na jiga-jigan jam'iyyae za su kunshi
   a. Shugaban jam'iyyar na jiha, wanda zai kasance a matsayin shugaban jiga-jigan jam'iyyar.
   b. Mataimakin shugaba;
   c. Gwamnan jihar da mataimakin gwamna, 'ya'yan jam'iyyar;
   d. Shugaban majalisar dokoki na hija da mataimakin shugaba da shugaban masu rinjaye da na marasa rinjaye da mai tsawatarwa da mataimakin mai tsawatarwa na majalisar dokokin jiha na jam'iyyar
   e. Wakilan kwamitin zattaswa na jam'iyyar na qasa daga suka fito daga jiha'
   f. Sakataren jam'iyya na jiha;
   g. Mataimakin sakataren jam'iyya na jiha;
   h. Mai bada shawara kan harkokin shara'a na jam'iyyar;
   i. Shugaban 'yan kasuwa na jiha;
   j. Shugaban daliban reshen daliban jam'iyyar na jiha; da
   k. Shugaban manoma na jiha.

AYYUKA

2) Rukunan jiga-jigan jam'iyya na jiha za su rinqa ganawa ne lokaci zuwa lokaci don la'akari da batutuwan da suka shafi jam'iyya a jiha ko qasa.

TARUKAN KWAMITIN JIGA-JIGAN JAM'IYYAR NA JIHA

3) Rukunin jiga-jigan jam'iyya na jiha za su riqa ganawa ne qasa da sau daya a kowanne watanni uku na kowacce shekara, tare da shugaba.
4) Za a gudanar da wani taron jiga-jigan jam'iyyar na jiha na musamman a duk sanda biyu bisa uku na wakilan kwamitin jiga-jigan tarayyar suka buqa ci hakan kuma irin wannan taron zai kasance ne a cikin mako guda da neman bukatar yin taron.
5) Adadin wakilan kwamitin jiga-jigan jam'iyyar na jiha daya bisa uku ne ake sa ran daga shiyyar dan majalisar magabata uku da ke jiha kuma bangaren maiya rijaye ne zai zattas da duk wani qudiri.

## MAJALISAR DATTAWAN JAM'IYYA NA JIHA

28

1) Zai zamana akwai majalisar dattawa na jam'iyyar a jiha da ba za su gaza 'ya'yan jam'iyyar tara (9) ba, kuma an tannadar da cewa:
    a. Kowanne Wakilin majalisar dattawa ba zai gaza shekaru arba'in da biyar ba;
    b. Su ne amintattun jam'iyyar mutane daal'umma ke muntuntawa; kuma
    c. Sun kasance 'ya'yan jam'iyyar tsawon shekaru hudu bayan kafa jam'iyyar da shekaru niyar, wato sun fi kowa dadewa a jam'iyyar

AYYUKAN MAJALISAR DATTAWAN JAM'IYYAR NA JIHA

2) Majalisar dattawan, kamar yadda tsarin mulkin jam'iyyar ya tanadar, za ta kasance ne mai:
    a. tabbatar sahihancin daukacin ayyukan jam'iyyar na jiha;
    b. Sasanta tsakanin manyan vangarorin tafiyar da jam'iyyar daban-daban da ke jiha;
    c. Sasanta tsakanin fallayen gwamnati na majalisar zattaswa da ta dokoki na jam'iyyar, da shiga tsakanin 'ya'yan jam'iyyar na jiha;
    d. Tabbatar da xa'a da biyayya a tsakanin 'ya'yan jamiyyar ta hanyan kiyayewa da bin
        i. Tanade-tanaden kundin tsarin mulkin jam'iyyar .
        ii. Da kaucewa ayyukan cin manar jam'iyya ta kowacce hanya;
        iii. Rashin Biyayya da sakace wajen aiwatar da umurni duka na jam'iyyar ko tafiyar da ofishin jam'iyyar;
        iv. Nuna rashin da'a da ya haxa da kawo rudani a wajen tarukan jam'iyya.
        v. Karya qa'idoji da matakan jam'iyya da suka hada da qin zuwa wurin taruka, da ayyukan yada manufofin cin amanar jam'iyya da duk wasu ayyukan da ka'iya wargaza zaman lafiya da nakasa manufofi da qudirorin jam'iyyar; har wa yau

e. Kwamitin dattawa za rinqa tallafawa wajen tantance 'ya'yan jam 'iyyar da ke neman muqaman gwamnati ; da
f. Tafiyar da sauran irin waxannan ayyuka da kwamitin zattaswa r jam'iyya na jiha zai daura masa.

3) Wakilan majalisar dattawam jam'iyyar zai kasance ne:
   a. Wanda kwamitin amintattu na jam'iyyar ya nada; kuma
   b. Kwamitin amintattun jam'iyyar ne ke da hurumin tsige shi daga ofis bayan samun shi da laifukan aikata ba daidai ba; sannan
   c. Yana da damar ajiye matsayin wakilin majalisar ta hanyar miqa takardar ajiye aikin ga shugaban kwamitin amintattu na jam'iyyar
   d. Zai iya rasa matsayin wakilin majalisar dattawa ne muddin:
      i. Jam'iyya ta kore ta/shi; ko
      ii. An tsige ta/ shi daga ofishin dayaba ta/shi damar zama wakilin majalisar .

TARUKA

4) Majalisar dattawa za ta gana ne bisa buqata shugabanta ko buqatar yin taron daga rabin wakilan majalisar zattaswar jam'iyyar da ya buqaci yin irin wannan taron.
5) Taron majalisar dattawan ana sa ran ya kasance ya samu halarcin wakilan majalisar biyu bisa uku.

**SASHI NA VII**

BABBAN TARON JAMIYYAR NA QASA

29

1) Zai zamana akwai wani babban taron jam'iyyar na qasa da zai qunshi:
   a. Shugaban jam'iyyar na qasa wanda zai kasance shugaban taron da sauran wakilan majalisar zattaswa ta qasa a jam'iyyar
   b. Shugaban qasar tarayyar nijeriya da mataimakin shugaban qasa wanda suke a matsayin 'ya'yan jam'iyyar;
   c. Wakilan majalisar dokiki kuma 'ya'yan ma'iyyar;
   d. Gwamnonin jihohi da mataimakan gwamnonin jihohi na jam'iyyar.
   e. Daukacin 'yan takarar gwamna na jam'iyyar, wadanda za su kasance wakilan babban taron kai tsaye.
   f. Wakilan majalisar dokokin jihohi na jam'iyyar wadanda za su kasance wakilan zave na babban taron
   g. Wakilan kwamitin amintattu;
   h. Shugabannin jam'iyyar na jiha da sakatarorin hadi da na babban birinin tarayyar Abuja.
   i. Shugabannin jam'iyyar na yankunan qananan hukumomi;

j. Wakilan zabe daya daga kowacce qaramar hukuma da babban taron waramar hukuma ya zaba don babban taron na qasa.
k. Daukacin zababbabun shugannin majalisar yankunan qananan hukumomi da ke qarqashin jam'iyyar;
l. Tsoffin wakilan kwamitin zattaswa na qasa, da suka kasance a jam'iyyar.
m. Tsoffin shugabanni da mataimakan shugabannin majalisar wakilai ta tarayya da sauran manyan jam'ian majalisar dodkoki na qasa da ke qarqashin jam'iyyar.
n. Shugabannin daliban jam'iyyar youth party na jihohi;
o. Shugabannin rassan jam'iyyar na qasashen waje;
p. Shugabannin kasuwanni na jam'iyyar; da
q. Shugabannin manoma na jam'iyyar na ayyukan babban taron jam'iyyar na qasa.

AYYUKAN BABBAN TARON JAM'IYYAR NA QASA

2) Babban taron jam'iyyar na qasa shi zai kasance qololuwa na tafiyar da tanade-tanaden kundin tsarin mulkin jam'iyyar kuma zai kasance mai wakiltar manufofi da qudirorin mulkin uwar jam'iyyar;
3) Kula da daukacin ayyukan da kundin tsarin mulkin jam'iyyar ya dorawa kowanne reshe na jam'iyyar ta hanyar fayyace tanade-tanaden kundin, tar on har way au zai zano matakin qarshe na zattas da duk wasu batutuwa da suka shafi ayyukan daukacin jam'iyyar da jami'anta kuma bangarorin tafiyar da jam'iyyar za su kasance masu tafiyar da ayyukan sune daidai da yadda matakan babban taron na qasa ya iyakance.
4) Babban taron jam'iyyar na qasa zai samar da wata hikimar da za a dorawa alhakin tafiyar da wadannan ayyukan kamar haka:
   a. Zabe da cire jami'an jam'iyyar na qasa;
   b. Fayyace dan takaran shugabancin qasa na jam'iyyar;
   c. Bukata da kavar rahotanni daga kwamitin zattaswa na qasa da sauran kwomitocin ko bangarorin jam'iyyar don daukar mataki da ya dace akan rahotannin
   d. Kafa kwamitoci idan buqatar hakan tare da basu karfin ikon tafiyar da ayyukan da aka ga ya cancancesu .
   e. Lura da matakai ko doka da duk gwamnatin jam'iyyar a matakin tarayya da jiha ko majalisar qaramar hukuma ke neman dauka don ganin sun yi daidai da manufofi da shirye-shireyn jam'iyyar; da
   f. Tabbatar da ganin 'yan takara na jam'iyyar da ke neman muqaman zauka daban-daban sun kiyaye da dokar qasa;
   g. La'akari da rahotannin rassan jam'iyya na jihohi da qananan hukumomi tare da daukar matakan da suka wajaba na kaewa da daukaka martabar jam'iyyar;
   h. Samar da wadatattub kudaden tafiyar da aikace-aikacen jam'iyyar;

i. Daukar matakan ladaftarwa na daukacin jami'ai da 'ya'yan jam'iyyar;
j. Lura da irin kwamitin zattaswar jam'iyyar na qasa zai kafa. .
k. Bita da yi wa kundin tsarin mulkin jam'iyyar gyaran fuska lokaci zuwa lokaci, idan buqatar hakan ta taso, kuma qarfin ikon babban taron na qasa zai kasance ne mara shamaki.
l. Wakilta
m. Daukar sauran wasu matakain gaggawa da samar da hanyoyin tabbatar da qudirorin jam'iyya.
n. Nada masu binciken kudi na waje don biciken asusun jam'iyya
o. La'akari da kudaden haraji na shekara-shekara da kowanne dan' jam'iyya zai biya dan daidaita kudaden harajin da za a tura skatariyar jam'iyyar ta qasa;
p. Bita da warware ko soke duk wani matakin doka da jami'an wani vangare ko reshen jam'iyyar suka dauka; da
q. Duk sauran wasu matakan iko da suka savawa tanade-tanaden kundin tsarin mulkin jam'iyyar.

TARUKA

5) Adadin 'ya'yan jam'iyyar da ake sa ran su halarci babban taron jam'iyyar na qasa, za su kasance ne biyu bis uku.
6) Babban taron jam'iyyar na qasa zai rinqa gudana ne a kowacce shekara hudu (4), kuma kundin ya tanadar da cewa a kowacce shekara da za a gudanar da babban taro, babu wani taron jam'iyya da zai kasance;
7) Tsarin babban taron jam'iyyar zai kasance a daidai da qa'idojin demokaradiyya
8) Za a iya gudanar da babban taron na qasa musamman a kowanne lokaci idan kwamitin zattaswar jam'iyyar ko niyu bisa uku na rassan jam'iyyar na jihohi suka buqaci haka; kuma babban taron zai tattauna ne akan wasu batutuwa na musamman da aka bayyana a sanarwar kiran babban taron.

9) TARON JAM'IYYA NA QASA

30

1) Za a rinqa gudanar da wani babban taron jam'iyyar wanda zai qunshi:
   a. Shugaban jam'iyyar na qasa wanda zai kasance shugaban babban taron da sauran wakilan kwamitin zattaswa qasa;
   b. Shugaban qasa da mataimakin shugaban qasan tarayyar Nijeriya, 'ya'yan Jam'iyya
   c. Wakilan majalisar dokoki na qasa da ke jam'iyyar;
   d. Gwamnoni da mataimakan gwmanonin jihohi 'ya'yan jam'iyyar da ke jam'iyyar
   e. Daukacin 'yan takaran gwamna na jam'iyyar wadanda za su kasance wakilan zabe ga taron

f. Wakilan majalisar dokoki na jihohi wanda su ma za su kasance wakilan zave a babban taron da
g. Wakilan kwamitin amintattu;
h. Shugabanni da sakatarorin jam'iyyar na jihohi hadw da na babban Birnin tarayya Abuja
i. Shugabannin jam'iyyar na yankunan qananan hukumomi; da
j. Za a zabi wakilin zabe daya ne a kowacce qaramar hukuma
k. Tarukan qananan hukumomi don shiryawa babban taron;
l. Daukacin zababbun shugabannin majalisar gundumoni.
m. Daukacin kwamitocin zattaswar jamiyyar na gunduma
n. Za zabi wakilin zabe daya ne a matakin kowacce gunduma don babban taron;
o. Tsoffin wakilan majalisar zattaswa na qasa da ke jam'iyyar; da
p. Tsoffin shugabanni da mataimakan shugabannin majalisar magabata da tsoffin wakilai ta qasa da sauran jami'an majalisar dokoki na qasa da ke jam'iyyar'
q. Sgugabannin daukacin bangaren daliban jam'iyyar
r. Za a zabi wakili daya daga kowacce reshen qungiyar daliban jam'iyyar don babban tar on;
s. Shugabannin rassan jam'iyyar na qasashen waje;
t. Za a zabi wakili daya daga kowacce reshen jam'iyyar na qetare; da
u. Shugabannin daukacin qungiyoyin manoma ta jam'iyyar;
v. Za a zabi wakili daya daga kowacce qungiyarmanoman jam'iyyar;
w. Shugabannin daukacin qungiyar ma'aikata na jam'iyyar;
x. Za a zabi wakili guda daya daga kowacce qungiya na ma'aikatan jam'iyyar;
y. Shugabannin daukacin qungiyoyin 'yan kasuwa na jam'iyyar;
z. Za a zabi wakili daya daga kowacce qungiyar 'yan kasuwan jam'iyyar,

WAKILAN ZABE

2) Don cimma burin babban taron jam'iyyar wajibi ne daukacin wakilan zaben su kasance wadanda suka cancanta da duk wani nadi.
   a. Wajibi ne a sami daukacin wakilan zaben masu rike da duk wani muqaman shugaba;
   b. Kowanne wakilin zabe sa ya kasance, 'dan jam'iyya
      kamar yadda kundin ya tanadar a sashi na (7) na neman zama dan' jam'iyya.
   c. Babu wani mutum da zai kasance a matsayin wakilin zabe na jam'iyyar fiye da daya;
   d. Kowanne wakilin zabe wajibi ne ya kasance dan' jam'iyyar da aqalla watanni 12 (twelve); da

e. Daukacin wakilan zaben na da 'yancin kada quri'arsu a wajen babban taron jam'iyyar;

AYYUKA

3) Ayyukan babban taron jam'iyyar sun hada da:
   a. Yin la'akari da amincewa da manufofi da shirye-shiryen jam'iyyar, kuma za a iya sakewa ko yin gyaran fuska ga manufofin da babban taron jam'iyyar na qasa ya samar idan aka sami wanda ya fi shi;
   b. Don la'akari da amincewa da canje-canjen da suka yi daidai da manufar jam'iyyar;
   c. Zattaswa da shawarwari da rahotannin;
   d. Samar da qudirorin na wucin gadi ko na gaggawa;
   e. Kula da manufar rahotanni da daftarin rahotanni a matsayin wani bangaren tafiyar da shirye-shiryen jam'iyyar;
   f. Da shiryawa da gabatar da rahotanni da shawarawari don neman sabon abin cewar babban taron jam'iyyar na qasa;
   g. Don shawo kan matsalolin da qananan bangarorin jam'iyyar suka miqa masa; da
   h. Da amincewa da kasafin kudin jam'iyyar na shekara-shekara;

KADA QURI'A

4) Kada quri'ar amincewa da shawarwari da rahotanni da yin gyaran fuska da neman wata buqata na babban taron jam'iyyar zai kasance ne ta hanyar nuna hannaye ko katin dan' jam'iyya ko ta hanyar wata hanya ta na'urar zamani.
5) Za a amince da mahimman batutuwan babban taron ne ta hanyar kada quri'a

TARUKA

6) Adadin 'ya'yan jam'iyyar da ake sa ran su halarci babban taron na qasa, sun kai biyu bisa uku kuma bangaren mafiya rinjaye ne za su zattas da duk wani qudiri.
7) Za a rinqa gudanar da babban taron jam'iyyar na qasa ne shekara-shekara da nufin bitar kwazon jam'iyyar da ke shugabanci a kowanne mataki da warware matsalar da ke shafar manufofin jam'iyyar.

**KWAMITIN BA DA SHAWARWARI NA JAMIRRAR**

31

(1) Za a samar da wani kwamitin bad a shawarwari kan daidaito,kuma aikinsa zai kasance ne:
   a. Samar da shawarwari masu ma'ana ga kwamitin zattaswa na qasa da na amintattu na ja'iyyar a kan batutuwan da suka jibanci daidaito;
   b. Ba da shawarwari ga kwamitin zattaswa na qasa da na amintattun jam'iyyar na qasa kan hanyoyin daya kamata abi wajen inganta tsarin shigar da naqasassu cikin harkokin jam'iyyarda na ayyuka gwamnati;
   c. Samar da shawarwari ga kwamitin zattaswa da na amintattu na qasa na jam'iyyar kan yadda za a tabbatar da lumana da mutunta juna a tsakanin qabilu da addinai;
   d. Samar da tsare-tsare da shirye-shiryen ilmantarwa a wayar da kai kan yadda za a gusar da batun nuna qabilanci da daidaito a harkokin jam'iyya da ayyukan gwamnati;
   e. Aiwatar da ayyuka da majalisar zattaswar jam'iyyar ta qasa da na kwamitin amintattu na qasa ka'iya dora masa/ta idan buqatar hakan ta taso.
(2) Za a kafa kwamitin bada shawarwari kan daidaito na jam'iyyar ne da wakilan jam'iyyar da keda rigista shida (6) daga kowacce shiyya, wanda kwamitin zattaswa na qasa zai zaba.
(3) Wakilan kwamitin ba da shawarari kan daidaito na jam'iyyar na iya rasa muqamansa ne idan:
   a. Shawarwain kwamitin amintattun jam'iyyar na qasa ya tsige ta/shi daga ofis bias dalili na aikata ba daidai ba; ko
   b. Ta/ya bar jam'iyyar ko an koreshi daga jam'iyyar; ko
   c. Ta/ya ajiye muqaminta hanyar miqa wasiqa akan batun ga shugaban kwamitin amintattun jam'iyyar na qasa; ko
   d. A cire ta/ko ko ta/ya ajiye muqamin daya ba ta/shi dammar kasancewa wakilin kwamitin
(4) Duk wakilin jam'iyyar da za kasance daga cikin wakilan kwamitin na da shawarwarin jam'iyyar na qasa kan daidaiton qabilanci ai ya cancanta ta hanyar cika wadannan sharuddan kamar haka:
   a. Sai ta/ya kasance amintacce a cikin al'umma; kuma
   b. Ta/ya zamto ta/yana a jam'iyyar da aqalla shekaru uxu (4) bayan yiwa jam'iyyar rigista da sama da shekaru biyar;
(5) Kwamitin bada shawarwari na jam'iyyar kan daidaito na qasa zai gana ne idan:
   a. Shugaban kwamitin ya yi kirar gudanar da taron kwamitin; ko kuma
   b. Shugaban kwamitin zattaswar jam'iyyar na qasa ya buqaci gudanar da wani taro da kwamitin; ko
   c. Kuma shugaban kwamitin amintattu ya buqaci gudanar da wani taro da kwamitin; ko
   d. Kwamitin zattaswar jam'iyyar na qasa da na amintattu na qasa sun buqaci gudanar da taron da kwamitin ta hanyar zattas da shawarwari akan batun.

(6) Adaddin tarukan kwamitin zaikasance ne biyu bisa uku $^2/_3$ na wakilansa.
(7) Kuma dole ne kwamitin bad a shawarwarin ya rinqa la'akari da ra'ayoyin marasa rinjaye a duk wata shawara da zai fitar ko ya bada

## KWAMITIN ZATTASWAR JAM'IYYAR NA QASA

32

(1) Za a samar da wani kwamitin zattaswar jam'iyyar na qas:

a. Shugaba na qasa;
b. Mataimakin shugaba na qasa;
c. Sakatare na qasa;
d. Mataimakin sakatare na qasa;
e. Mai bada shawara kan harkokin shara'a na qasa;
f. Mataimakin mai bada shawara kan harkokin shara'a na qasa;
g. Sakataren yada labarai;
h. Mataimakin sakataren yada labarai;
i. Ma'aji na qasa;
j. Mataimakin ma'aji na qasa;
k. Sakataren shirye-shirye na qasa;
l. Mataimakin sakataren shirye-shirye na qasa;
m. Mai binciken kudi na qasa;
n. Mataimakin mai binciken kudi na qasa;
o. Sakataren kula da tsare-tsare da manufofin jam'iyyar na qasa;
p. Mataimakin sakataren kula da tsare-tsare damanufofin jam'iyyar na qasa;
q. Sakataren kudi na qasa;
r. Mataimakin sakataren kudi na qasa;
s. Shugaba daliban reshen Youth Party (SYP);
t. Shugaban reshen jam'iyyar na manoma;
u. Shugaban reshen jam'iyyar na 'yan kasuwa na qasa;
v. Daukacin wakilan kwamitocin amintattu; da
w. Tsoffin jiga-jigan wakilan jam'iyyar shida

(2) Kwamitin zattaswar jam'iyyar na qasa zai zamto ne mai:

a. Alhakin tafiyar mulkin jam'iyyar na yau da kulum;
b. Zai rinqa zattasda doka daya taso cikin gaggawa a madadin babban taron jam'iyyar na qasa tare da ganashi da babban taon jam'iyyar na qasa don warwarewa kacokan;
c. Gudanar da saran irin wannan ayyukan da babban taron na qasa zai iya dora masa idan buqatar hakan ta taso;

d. Kiran babban taron jam'iyyarna qasa ta hanyar nada wani kwamitin shirye-shirye da zai rinqa bi kwararo-kwararoyana yada bayanan babban taron na qasa tare da tabbatar da ganin an sanya abin day a shafi 'ya'yan jam'iyyarcikin batutuwan da za a aiwatar wurin taron;
e. Daukacin matakai a qa'idojin babban taron jam'iyyar na qasa;
f. Dubawada jan sahun ayyukan jam'iyyar da daukacin vanarorinta da suka hada da na wakilan qasa, hija da qaramar hukuma; da
g. Tabbatar da ganin kowani bangaren jamiyyar na tafiyar da ayyukansa a demokaradiyyance kuma yadda ya kamata;
h. Rushe duk wani kwamitin zattaswar jam'iyya na jihad a nada wani kwamitin riqon kwarya da zai tafiyar da ayyukan jam'yyar har sai an zabi wani sabon kwamitin zattaswar jam'iyyar a duk inda ke buqatar hakan, kuma bias tanadin da kundin ya samar ya nunar da cewar daga lokacin da aka rushe kwamitin zuwa ranar zaven sabbin wakilan kwamitin zattaswar jam'iyyar ba zai wuce watanni uku (3) ba;
i. Shirya rahotanni da kasafin kudi don amincewar babban taron jam'iyyar na qasa;
j. Samar da manufofi da shirye-shirye don samun amincewar babban taron jam'iyyar na qasa;
k. La'akari da kiraye-kiraye da sauran wasu batutuwa ba reshen jam'iyyar na shiyyoyi da jihohi tarayyar kasar nan suka gabatar mata;
l. Gindaya qa'idojin tabbatar da da'a da zai shafi daukacin bangarori da wakilan jam'iyyar;
m. Bisa tanadin wannan kundin tsarin mulki, sharuddan da qa'idojin zabe su zasu yi jagorancin gudanar da duk zabukan daukacin muqaman ofis-ofis na jam'iyyar a kowacce mataki da duba tsarin zaben 'yan takaran jam'iyyar masu neman muqamai;
n. Shawo kan sharuddan ayyukan na ma'aikatan gwamnati na jam'iyyar daidai da tsari;
o. Yin dokoki na bai daya don amincewar babban taron jam'iyyar na qasa;
p. Shawo kan duk sauran batutuwan da babban taron jam'iyyar na qasa ko kwamitin amintattu ya gabatar masa;
q. Kafa bangarorin samar da kwamitin wucin gadi ko kwamitin da zai kulada jam'iyyar;
r. Tabbatar da kulada daukacin kadarorin da dukiyar jam'iyyar a duk inda suke;
s. Tuntubar kwamitin amintattu da nada shugabannin jam'iyyar muqaman masu martaba kuma duk wanda aka baiwa wannan girma na da 'yancin halarar kowane taron bangarorin jam'yyar;
t. Lura da matakai da tsare-tsare da shiry-shiryen da dokokin da gwamnatin tarayya da ta jiha na jam'iyyar suka dauka don daukar matakan tabbar da

ganin sun yi daidai da muradun jam'iyyar ta hanyar bada shawarwari ko daukar matakan da suka dace.

u. Samar da wadatattun kudaden tafiyarwa da kawo morewar jam'iyyar;
v. Ba da shawara ga babban taron jam'iyyar na qasa kan kudaden day a kamata 'ya'yan jam'iyya su biya duk shekara.
w. Samar da wata martaba da zata maganta qudirorin jam'iyyar

<u>TARUKA</u>

(3) Kwamitin zattaswar na qasa zai gana aqalla sau daya a kowanne watanni uku na farkon shekara a gaban shugaban Jam'iyyar na qasa ko bisa buqatar biyu bisa uku na 'ya'yan jam'iyyar, amma za a sanar da shugaban jam'iyyar da aqalla kwanaki bakwai kafin taron; inda shi kuma zai kira taron gaggawa na tattaunawa akan batutuwan taron.

(4) Adadin wakilan kwamitin zattaswar zaikasance ne biyu bias uku ($^2/_3$) wadanda suka fito daga shiyyoyin tarayya daban-daba, kuma bangare mafi rinjaye ne za zattas da duk wani qudiri.

(5) Ba tare da la'akari ba, qarami sashi na ku (3) a baiwa shugaban jam'iyya na qasa dammar kiran taron gaggawa a kowanne lokaci, haka nan ma biyu bisa uku na 'ya'yan jam'iyya na da dammar nema bukatar ayi taron, amma saidai za a sanar wa shugaban jam'iyyar na qasa aqalla kwanaki bakwai kafin taron.

## SASHI NA VII

## KWAMITIN AMINTATTU

33

(1) Za a samar da kwamitin amintattu na kasa ta jam'iyyar (BOT) wanda zai qunshi:

a. Daukacin tsoffin shugabannin qasa da mataimakan shuwagaban qasa wadanda suke kan mulki da wadanda suka gushe a matsayin su na 'ya'yan jam'iyyar da basu bar jam'iyyar ba;
b. Daukacin shoffin shugabannin jam'iyyar na qasa da mataimakan shugabannin qasa da sakatarorin jam'iyyar na qasa, wadanda ke a jam'yyar;
c. Daukaci tsoffin shugabannin majalisar dattawa ta qasa da tsoffin shugabannin majalisar wakilai ta tarayya wanda basu bar jam'iyyar ba;
d. Wakilai biyu (2) dasuka assasa jam'iyyar da aka bayyana a wannan kundin tsarin mulkin;
e. Mutane da basu wuce goma sha biyu (12) ba wadanda suka bada gudummawa gaya wajen gina jam'iyyar wanda kwamitin amintattu yai yi amanna dasu;

ZABE DA WA'ADIN JAMI'AI DAWKILAN JAM'IYYA

(2) Kwamitin amintattu na jam'iyyar zai:

a. Zabi shugaba da sakatare daga wakilansa;
b. Ba tareda nuna fifko ba, kundin tsarin mulkin jam'iyyar zai tabbatar da ganin shugaba da sakatare masu shedar da'a da gaskiya da adalci wadanda suka bada gudummawa sosai ga yan' jam'iyyar ne da aka zaba;
c. Tabbatar da ganin shugaba da sakataren kwamitin amintatu sun kwashe wa'adin shekara biyar (5) ba tare da qetarewa ba;

CANCANTAR DAN JAM'IYYA

(3) Kowanne mutum zai cancanci zama wakilin kwamitin amintattu ne idan har/yana da

a. Katin shedar zama dan jam'iyyar aqalla shekaru hudu bayan rigistar jam'iyyar da aqalla shekara biyar; da
b. Dogewa biyan kudaden haraji na jam'iyyar a kan lokaci; tare da
c. Kasancewa mai kyakkyawan dabi'a.

AYYUKA

(4) Kwamitin amintattu zai kasance mai aiki da tanade-tanaden wannan kundin tsarin Mulki, inda zai rinqa:

a. Tabbatar da tarbiya a daukacin harkokin jam’iyyar ta hanyar samun damar karkato da duk wani jami’in jam’iyyar da ya aikata ba daidai ba, da hakan ya saba muradun jam’iyyar;
b. Tabbatar da da’ar ‘ya’yan jam’iyyar da tsare martabar jam’iyyar a idon ‘yan Nigeria da harkokin siyasa masu tsafta;
c. Daidaitawa da shiryawa da bita da ba da shawarwari ga manufofi da shirye-shirye da harkokin jam’iyyar a matakin jam’iyyar na qasa.
d. Tsara hanyoyin samun kudaden jam’iyyar
e. Lura da kadarorin jam’iyyar;
f. Sa baki a rikicin da ka’iya wanzuwa tsakanin ‘yan majalisar zattaswa da na ‘yan majalisar dokokin da aka zaba qarqashin jam’iyyar;
g. Ba da shawarwari akan batutuwan jam’iyyar ga kwamitin zattaswar jam’iyyar na qasa;
h. Kafa tsarin tafiyar da harkokin ‘ya’yan jam’iyyar da kudi da na zabe;
i. Samar da tsarin kula da kwazon kwamitin zattaswar jam’iyyar na qasa.
j. Kada quri’ar amincewa ko qin amincewa da duk wani wakilin majalisar zattaswar jam’iyyar na qasa da ya gaza cimma kwazon da ake buqata;
k. Cire duk wani wakilin Kwamitin zattaswar da jami’in jam’iyyar na qasa ta hanyar amfani da shawarwarin ‘ya’yan jam’iyyar qasa da biyu bisa uku;
l. Dakatar da dan jam’iyyar da ya cancanci haka;
m. Tabbatar da dorewar da’a da kiyayewa da martabar da muradun jam’iyyar na wadanda suka kafa jam’iyyar.
n. Halartar duk wani tarukan bangarorin jam’iyyar; da
o. Tafiyar da duk sauran harkokin jam’iyyar da kwamitin zattaswar jam’iyyar ka’iya dora ma kwamiti.

(5) Kwamitin amintattu shi zai rinqa tafiyar da qa’idojinsa kuma zai kasance mai tsara dokar kula da da’a ga wakilansa.

TSARIN TSIGEWA DA AJIYE AIKI

(6) Duk wakilin kwamitin amintattu na jam’iyyar za a:

a. Rinqa cire shi ne daga ofis bisa shawarawarin da aka zattas a babban taron jam’iyyar na qasa bayan karbar shedar aikata ba daidai ba daga kwamitin amintattun jam’iyyar na qasa;
b. Ko idan ya ajiye matsayinsa na wakilin kwamitin amintattu ta hanyar miqa takardar ajiye aikin ga shugaban jam’iyyar;

(7) Bisa tanadin wannan kundin tsarin mulkin jam’iyyar, wakilin kwamitin amintattun zai iya rasa matsayinsa na dan kwamitin ne; idan

a. An koreshi daga jam'iyyar; ko
b. Cire shi daga ofis na nadi ko zabe da ya bashi ikon zama dan kwamitin qarqashin tanadin Kundi n tsarin mulkin jam'iyyar;

(8) Za a sake zaben wadanda za su cike duk wani gibi da aka samu cikin kwamitin amintattun.

TARUKAN KWAMITIN AMINTATTU

(9) Kwamitin amintattu zai gana a gaban shugaban kwamitin ko bisa buqatar in hakan daga mafi akasarin wakilan kwamitin ko kwamitin zattaswar jam'iyyar na qasa suka zattas na shirya irin wannan taron.

(10) Adadin kwamitin amintattu zai kasance biyu bisa uku na wakilansu, kuma kaso mafi rnijaye ne zasu zattas da duk wani qudiri.

**BABI NA BIYAR SASHI NA IX**

QARFIN IKO DA AYYUKAN JAMI'AN JAM'IYYAR MANYAN JAMI'AN JAM'IYYAR NA QASA.

32.

Zai kasance akwai manyan jami'an jam'iyyar na qasa, maza da mata masu kwazo da kwarewa da nagarta da suka cancanta, wadanda za su tafiyar da ayyukan da wannan kundin tsarin mulkin ya dora masu

SHUGABAN JAM'IYYAR NA QASA

35

Za a samar da wani shugaban jam'iyyar na qasa wanda zai kasance shugaban bangaren zattaswa na jam'iyyar kuma ayyukanta/ shi zai kasance

1. Kira da shugabantar tarukan kwamitin zattaswa da na jiga-jigan jam'iyyar na qasa , har ma da babban taron jam'iyyar na qasa
2. Samar da kyakkyawan shugabanci da jajjircewa da tafiyar da aikace-aikacen jam'iyyar qarqashin kulawar kwamitin zattaswar jam'iyyar na qasa.
3. Bunqasawa da kare martaba da manufofi da shirye-shiryen jam'iyyar; da samar da tsare-tsare da qudirorin da shuga shirye-shirye da aikace-aikacen jam'iyyar a madadin kwamitin zattaswar jam'iyyar na qasa;
4. Daura ayyuka ga duk wani jami'i ko wakilin jam'iyyar;
5. Da dora wakilcin mataimakin shugaban jam'iyyar bisa umurin iko sa;
6. Kada quri'ar amincewa ko qin amincewa idan buqatar hakan ta zama wajibi;
7. Gabatar da cikakken bayani kan matsayin jam'iyyar da yanayin tsarin siyasarta baki daya ga babban taron jam'iyyar na qasa.
8. Tabbatar da ganin ana kiyayewa da tanade-tanaden kudin tsarin Mulki na jam'iyyar da yin duk abu mai yiyuwa na inganta cigaban jam'iyyar

MATAIMAKIN SHUGABAN JAM'IYYAR NA QASA

36

1. Za kasance akwai mataimakin shugaban jam'iyyar na qasa wanda zai fito ko dai daga Arewaci ko kudancin qasar nan, hakan zai dogara ne da wani bangaren qasar nan, shugaban jam'iyyar na qasa;
2. Mataimakin shugaban jam'iyyar na qasa zai kasance ne mai tafiyar da ayyuka kamar haka:
    a. Tallafawa shugaban jam'iyyar na qasa wajen tafiyar da ayyukan ta/sa;
    b. Riqe matsayin shugaban jam'iyyar na qasa idan baya nan; da tafiyar da sauran ayyukan jam'iyyar da za a dora mashi.

SAKATAREN JAM'IYYAR NA QASA

37.

1. Zai kasance akwai sakataren jam'iyyar na qasa da zai zamo babban jami'in Mulki kuma akanta na jam'iyyar , wanda tafiyar da ayyukan kamar haka:
    1. lura da ayyukan yau da kullum na jam'iyyar;
    2. tafiyarwa ko tsara yadda za a gudanar ko nadar bayanan jam'iyyar; ba da wa'adin gudanar da tarukan kwamitin zattaswar jam'iyyar na qasa;
    3. Ajiye duk wasu bayanan tarukan babban taron jam'iyyar na qasa da na kwamitin zattaswa da na jiga-jigan jam'iyyar da duk sauran wasu bayanan jam'iyyar;
    4. Ba da rahotannin aikace-aikacen jam'iyyar na duk shekara-shekara A rubuce ga majalisar zattaswa da babban taron jam'iyyar na qasa;
    5. Tabbatar da shawarwari da umurnin babban taron jam'iyyar na qasa da kwamitin zattaswa da na jiga-jigan jam'iyyar na qasa tare da tabbatar da ganin daukacin bangarorin jam'iyyar na gudanar da ayyukansu akan lokaci kuma yadda ya kamata.
    6. Shawartar shugaban jam'iyyar na qasa kan tafiyar da ayyukan ofishin ta/shi;
    7. Tafiyar da duk sauran wasu ayyuka da kwamitin zattaswa da na jiga-jigan jam'iyyar na qasa ko babban taron jam'iyyar da shugaban jam'iyyar na qasa ka'iya dora mata/shi
    8. Sakataren jam'iyyar na qasa shi zai kasance sirrin jam'iyyar.

MATAIMAKIN SAKATAREN JAM'IYYAR

38). Zai kasance akwai mataimakin sakataren jam'iyyar na qasa da zai rinqa tallafawa sakataren jam'iyyar wajen tafiyar da ayyukansa kuma zai yi aiki a madadinsa idan baya nan.

MAI BADA SHAWARA KAN HARKOKIN SHARI'A

39) Zai kasance akwai mai bai wa jam'iyyar shawara kan harkokin shawara na qasa wanda zai zamto lauya mai kwarewa ta qasa da shekara biyar wanda ayyukansa za su kasance kamar haka:

1. Baiwa jam'iyyar shawara kan harkokin shara'a;
2. Shi zai rinqa gudanar da shari'u da hukunci da kare duk matakan jam'iyyar da ya hada da na sauran bangarori da jami'anjam'iyyar ; da
3. Fassara dokoki, qa'idojin kundin tsarin mulkin jam'iyyar inda aka sami harshen damo.

MATAIMAKIN MAI BADA SHAWARA KAN HARKOKIN SHARA'A NA JAM'IYYAR NA QASA

(40) Zai zamana akwai mataimakin mai bada shawara kan harkokin shara'a na jam'iyyar wanda zai zamto lauya mai kwarewa ta qasa da shekara biyar, kuma ayyukansa zasu kasance ne tallafawa mai bada shawara kan shara'a na jam'iyyar tare da zamowa wakilinsa a duk lokacin da baya nan.

SAKATAREN YADA LABARAI NA QASA

(41)

1. Za a samar da sakataren yada labarai wanda ayyukansa za su kasance kamar:
   a. Mai tafiyar da daukacin batutuwan da suka shafi yada labarai da hurda da jama'a na jam'iyyar
   b. Yada bayanan matakai da shirye-shiryen jam'iyyar daidai da manufofin da qudirorin jam'iyyar.

   MATAIMAKIN SAKATAREN YADA LABARAI NA JAM'IYYAR
2. Zai kasance akwai mataimakin sakataren yada labarai na jam'iyyar wanda zai rinqa tallafawa sakataren yada labarai na jam'iyyar wajen tafiyar da ayyukans, da riqe masa gurbi idan baya nan.

MA'AJIN JAM'IYYAR NA QASA

(42)

1. Ma'ajin jam'iyyar na zai kasance ne mutumin kwarai mai shedar riqon amana inda ayyukansa za su kasance:
    a. Karva da ajiye daukacin wasu kudaden da aka samu a madadin jam'iyyar a asusun ajiyar jam'iyyar ba tare da bata lokaci ba da ajiye duk sauran littattafan cekin kudi da bayanan bankin jam'iyyar
    b. Tabbatar da kyakkyawar tsarin tafiyar da kudaden jam'iyyar;
    c. Tabbatar da ganin duk kudaden da jam'iyyar ta karba an ajiyesu a asusun jam'iyyar nan take idan kuma a aka cimma wani dalili na qin yin hakan to ana sa ran kudaden a biyasu ne cikin sa'o'I (48) da karbar su; da
    d. Shiryawa da gabatar da bayanan matsayin da asusun jam'iyyar ke ciki duk shekara da bada rahotannin asusun ga kwamitin zattaswar jam'iyyar na qasa lokaci zuwa lokaci;

MATAIMAKIN MA'AJI NA QASA

2. Za zamana akwai mataimakin ma'ajin jam'iyyar na qasa wanda zai rinqa tallafawa ma'ajin jam'iyyar na qasa wajen gudanar da ayyukansa da wakiltarsa in baya nan:

SAKATAREN SHIRYE-SHIRYE NA QASA

(43)

1. Zai kasance akwai sakataren tsare-tsare na qasa wanda zai rinqa gudanar da ayyuka kamar haka:
    a. Qirqiro da shirye-shiryen wayar da kan 'ya'yan jam'iyyar da na daukar sabbin ''ya'yanm jam'iyyar;
    b. Gano matsalolin jam'iyyar da nemo hanya mafita ga irin wadannan matsaloli;
    c. Daidaita daukacin bayanai da shawarwarin dabarun samun nasarar zabuka yadda ya kamata;
    d. Shirya duk aikace-aikacen jam'iyyar;
    e. Shirya zaben fidda dan takara ta tarukan ilmantarwa da qarawa juna sani da gangamin shirye-shirye don cimma qudirorin jam'iyyar
    f. Tuntubar rassan jam'iyyar don daidata shirye-shiryen cimma burin jam'iyyar na samun nasara daukacin zabuka.

MATAIMAKIN SAKATAREN SHIRYE-SHIRYE NA QASA

2. Zai kasanceakwai mataimakin sakataren shirye-shirye na jam'iyyar na qasa zai rinqa tallafawa sakataren shirye-shirye na qasa wajen gudanar da ayyukansa har da wakiltarsa idan baya nan.

MAI BINCIKEN KUXI NA QASA

(44)

1. Zai kasance akwai mai bin ciken kudi na qasa wanda ayyukansa za su kasance:
   a. Binciken daukacin littattafan cekin kudin jam'iyyar duk shekara da ba da rahoto ga kwamitin zattaswar jam'iyyar na qasa;
   b. Gabatarda asusun jam'iyyar da aka kamala bincikesa ga babban taron jam'iyyar na qasa; da
   c. Tafiyar da duk wasu ayyukan da majalisar zattaswar jam/iyyar na qasa ka'iya dora masa.

MATAIMAKIN MAI BINCIKEN KUDI

2. Zai kasance akwai mataimakin mai binciken kudin jam'iyyar na qasa da zai rinqa tallafawa mai binciken kudi na qasa wajen gudanar da ayyukansa, har ma da wakiltarsa idan baya nan.

SAKATAREN TSARA MANUFOFI DA DABARU NA QASA

(45) Zai zamana akwai sakataren tsara manufofi da dabaru na qasa, wanda ayyukansa zasu kasance:

1. Tafiyar da aikace-aikacen bangaren bincike da tsare-tsare na jam'iyyar;
2. Bai wa jam'iyyar bayanan kan bangaren bincike da tsare-tsaren jam'iyyar
3. Daukar babban daraktan sashin bincike da stara manufofi na jam'iyyar.
4. Gabatar da kasafin kudin jam'iyyar da sashin bincike da tsara manufofi ke buqata gaban jam'iyyar;
5. Tsara manufofi da shirye-shirye da za a gabatar don neman amincewar babban taron jam'iyyar na qasa
6. Tsara dabarun sadarwa da jam'iyyar ke buqata;
7. Kasancewa a matsayin shugaban majalisar gudanarwar sashin bincike da tsara manufofi na jam'iyyar.

MATAIMAKIN SAKATAREN TSARA MANUFOFI DA DABARU NA QASA

(46) Samar da mataimakin sakataren tsara manufofi da dabaru na qasa da zai tallafawa sakataren tsara Manufofi da badaru na qasa wajen gudanar da ayyukansa da mai wakilci idan baya nan.

SAKATAREN KUDI NA QASA

(47)

1. Zai zamana akwai sakataren kudi na qasa da ayyukansa za su kasance:
   a. Karba da ajiye bayanan daukacin kudaden haraji da gudummawar da aka biya ko baiwa jam'iyyar;

b. Shiryawa da gabatarda buqatar tara kudade ga jam'iyyar qarqashin hangen nesan kwamitin zattaswar jam'iyyar na qasa;
c. Kula matuqa da yin kasafin kudi da tafiyar da kasafin da ba da rahotan bayanan matsayin kudaden jam'iyyar;
d. Kare kadarorin jam'iyyar da tsara hanyoyin tafiyar da sha'anin kudi kulawar aikin gida; da
e. Samarwa da tsara manufofin samarwa jam'iyyar kudaden shiga;

MATAIMAKIN SAKATAREN KUDI NA QASA

2. Za kasance akwai mataimakin sakataren kudi na qasa da zai rinqa tallafawa sakataren kudi na qasa wajen gudanar da ayyukansa, da wakiltarsa idan baya nan.

SHUGABAN BANGAREN DALIBAN JAM'IYYAR YOUTH PARTY (SYP)

(48) Zai zamana akwai shugaban reshen daliban jam'iyyar wanda aikinsa zai kasance

1. Hada kan dalibai don cimma qudirorin jam'iyyar;
2. Qirqirowa da aiwatar da shirye-shirye da dabaru da ke da nufin samawa jam'iyyar goyon bayan daukacin daliban Nijeriya ; da
3. Kula da aikace-aikacen reshen daliban jam'iyyar;

SHUGABAN MANOMA NA QASA

(49) Zai kasance akwai shugaban manoma na qasa wanda aikinsa zai kasance:

1. Hada kan manoma don cimma qudirorin jam'iyyar;
2. Qirqirowa da aiwatar da shirye-shirye da dabaru da za su samawa jam'iyyar goyon bayan daukacin manoman Nijeriya ; da
3. Kula da aikace-aikacen shugaban jiha na rassan jam'iyyar na manoma;

SHUGABAN KASUWA NA QASA

(50) Zai kasance akwai shugaban kasuwa na qasa, wanda zai tafiyar da ayyuka kamar haka:

1. Hada kan 'yan kasuwa na kowanne bangare;
2. Qirqirowa da aiwatar da shirye-shirye da tsare-tsaren da za su samawa jam'iyyar goyon bayan daukacin 'yan kasuwa na Nijeriya ; da
3. Kula da aikace-aikacen shugaban rassan jam'iyyar na 'yan kasuwa;

TSOFFIN JAMI'AN (WAKILAN KWAMITIN ZATTASWAR JAM'IYYAR)

(51) Zai kasance akwai tsoffin wakilan jam'iyyar, wadanda za su zamto:

1. Ba su da wani muqami;

2. Halartar daukacin tarukan kwamitin zattaswar jam’iyyar na qasa;
3. Kada quri’ar amincewa ko qin amincewa da daukacin tarukan kwamitin zattaswar jam’iyyar na qasa; da
4. Gudanar da sauran duk wasu ayyuka da shugaban jam’iyyar na qasa ka iya dora masu.

## BABI NA SHIDA (6)

## TSARIN AJIYE AIKI KO CIRE JAMI’AN JAM’IYYAR NA QASA

(52)

1. Idan aka cire wani jami’in jam’iyyar na qasa ko ya ajiye aiki, nan take zai miqa daukacin bayanai da fayil-fayil da sauran kayayyakin jam’iyyar da ke wurin ta/sa ga sakataren jam’iyyar na qasa
2. Bangaren shugaban jam’iyyar na qasa kuwa, zai miqa madafun ikon jam’iyyar ne kacokal ga mataimakin jam’iyyar na qasa da zai kasance mai rikon shugaban jam’iyyar har lokacin da aka yi zaben cike gurbin shugaban jam’iyyar.
3. Sannan shi ma sakataren jam’iyyar na qasa idan lokaci ta faru akansa, zai miqa ragamar tafiyar da muqamin ne ga mataimakin sakataren jam’iyyar na qasa.
4. Wannan tanadi shi zai kasance abin da ake amfani da shi a sauran rassan jam’iyyar;

QARFIN IKON TAFIYAR DA MUQAMAI NA JAMI’AN SAURAN MATAKAI

(53)

1. Daukacin sauran jami’an jam’iyyar na matakan, jiha da qaramar hukuma da gunduma za su kasance ne masu karfin ikon tafiyar da ayyukan rassansu kamar yadda na qasa ke da shi.
2. Bisa tanade-tanaden wannan tsarin mulkin jam’iyyar , kwamitin zattaswar jam’iyyar na kowanne mataki na da iko na kafa kwamitoci idan buqatar haka ta wajaba tare da dora masu ayyukan da za su yi.
3. Kwamitin zattaswar jam’iyyar na dikkan matakai su za su kasance masu lura da bin qa’idoji da tsarin qasa.

WA’ADIN RIQE OFIS NA JAMI’AN JAM’IYYAR

(54)

1. Daukacin jami’an jam’iyyar na qasa da jiha da qananan hukumomi za su kasance a muqamin ofishin ne tsawon shekaru hudu kuma za su iya tsaya wa takarar neman sake zaben su.
2. Zaben jami’an jam’iyyar na qasa zai kasance ne a babban taron jam’iyyar na qasa, yayin da zabukan sauran qananan matakan jam’iyyar zai kasance ne a babban taron matakan daban-daban.
3. Za a iya kada quri’ar amincewa ko qin amincewa da kowanne wakilin kwamitin zattaswar jam’iyyar na kowanne mataki a wurin babban taron jam’iyyar na qasa na kowanne mataki shekara biyu na wa’adin wakilin kwamitin zattaswan, a yayin da inhar aka gaza amnincewa da wannan wakili za a sauya shi da wani a babban taron jam’iyyar na qasa. Tanadin kundin tsarin za a baiwa wannan batun kada quri’ar qin

amincewar watanni biyu don ta zagaya daukacin rassan jam’iyyar na matakai kafin babban taron jam’iyyar na qasa.

4. Kada qu ri’ar qin amincewar zata iya rashin nasara ne idan har mafi rinjayen ‘y’yan jam’iyyar suka qi amincewa da ida a babban taron jam’iyyar na qasa.
5. Duk wani jami’I da aka zaba a kwamitin zattaswar jam’iyyar na kowanne mataki zai iya ajiye aikinsa ne ta hanyar bada ; wa’adin kwanaki talatin na ajiye aikin a rubuce ga bangaren da abin ya shafa.
6. A duk sanda aka sami wani givin ofishi a jam’iyyar, majalisar zattaswar jam’iyyar za ta bi matakan da suka kamata wajen nada wani mutum daga yankin ko shiyya inda ofishin yake, har sai tsawan lokaci da aka gudanar da zaben cike gurbi.

HARAMCIN RIQE OFISHI BIYU

(55) Bisa tanadin wannan kundin tsarin Mulki, duk wani wakilin jam’iyyar da ke riqe da wani ofis na jam’iyyar a kowanne mataki, zai ajiye aiki ofishin idan har ya zamto mai kare aiki a wadannan muqamai kamar haka

1. Shugaban qasar tarayyar Nijeirya;
2. Mataimakin shugaban qasar tarayyar Nijeriya;
3. Ministan tarayyar Nijeriya; ko
4. Ministan tarayya; ko
5. Sakataren gwamnatin tarayyar; ko
6. Mai ba da shawara ta musamman ko mai taimakon na musamman ga shugaban qasa ko mataimakin shugaban tarayyar Nijeriya; ko
7. Wakilin majalisar dokoki ta qasa ko na jihohi; ko
8. Zama jakadan qasa;
9. Gwamnan jiha ko mataimakin gwamnan jiha; ko
10. Kwamishina, ko mai bada shawara ta musamman ko mai mai taimakawa na musamman ga gwamna ko mataimakin gwamna a wata jiha; ko
11. Shugaban qaramar hukuma ko mataimakin shugaban qaramar hukuma; ko
12. Duk wani aiki na dindindin ko nadin a matakin ayyukan gwamnatin tarayya ko jiha ko qaramar hukuma.

## BABI NA BAKWAI

## TSARIN ZABEN JAMI'AN JAM'IYYAR

(56)

1. Babban taron jam'iyyar na qasa da sauran na matakan jam'iyyar na jiha da yankin qaramar hukuma, za su kasance masu zabar jami'in tarayya na matakansu daban-daban, kamar yadda wannan kundin tsarin mulkin ya bayyana, amma, sai dai a zaven jami'an jam'iyyar zai kasance ne bisa bin tsarin shiyyoyin siyasa.
2. Duk wani dan jam'iyyar mai rigista da ya cika duk sharuddan zaben qarqashin wannan kundin tsarin mulkin tarayyar jam'iyyar da na kundin tsarin mulkin Nijeriya da sauran wasu dokoki da qa'idar da aka gindaya a kan haka, ya cancanci neman kujerar kowanne ofishin jam'iyyar.
3. Kwamitin zattaswar jami'iyyar na qasa ne zai amince da duk wasu sharuddan zabuka na kowanne ofishin jam'iyyar, daidai da tanade-tanaden wannan kundin tsarin Mulki.
4. Babu wani dan jam'iyyar da zai cancanci a miqa sunansa don zabe ko nadin kowanne ofishin jam'iyyar har sai ta/yana da rigistan da jam'iyyar da aqalla watanni sha biyu (12) sai idan har ya samu tantancewar kwamitin zattaswa.

**BABI NA TAKWAS**

**AYYANA DAN TAKARA DON ZABEN MUQAMAN SIYASA**

57

1. Kwamitin zattaswar jam'iyyar ta qasa, shi zai tsara qa'idoji da sharudda na ayyana 'yan takarar zabukan muqaman siyasa a kowanne mataki bisa bin tanadin dokar zabe da ke kundin tsarin mulkin Nijeriya na shekara 1999 da aka yi wa gyaran fuska kuma shi zai kasance mai cewa ta jituwa da za a iya samu wajen zabe tare da baiwa hukumar zabe ta qasa mai zaman kanta ko duk wata hukumar da abin ya shafa, haqiqanin jerin sunayen 'yan takaran jam'iyyar da za su fafata a kowanne zaben neman kujerar muqaman siyasa na qasar nan.
2. Bisa tanade-tanaden babi na IV na wannan kundin tsarin mulkin jam'iyyar, kwamitin zattaswar jam'iyyar ne zai kasance mai tafiyar da tsare-tsaren zaben 'yan takarar da zasu wakilci jam'iyyar a neman kujerar zabe ta kowanne mataki, ta wadannan hanyoyi
    a. Amincewa da wani tsarin gudanar da zaben fidda 'yan takarar jam'iyyar, a inda daukacin wakilan jam'iyyar da suka cancanta da ke jam'iyyar da aqalla watanni tara ke da ikon shiga zaben a gundumomi da suka yi rigista. Sannan duk wata sauyi da aka samu ciki akan haka wajibi ne kwamitin zattaswar jam'iyyar na qasa ta amince dashi.
    b. Amincewa da samar da wani tsarin zamani na kada quri'ar zaben 'yan takara da za su tsaya neman, muqaman gwamnati a inda ake buqatar hakan;
    c. Doriya akan batun cika shekarun tsayawa takarar neman muqaman gwamnati, duk wanda ke d sha'awar tsayawa takara qarqashin Jam'iyyar Youth Party, wajibi ne ya zama dan jam'iyyar da aqalla watanni sha biyu (12) tun daga lokacin da hukumar zabe ta qasa ta tsaida na gudanar da manyan zavuka, sannan duk wani sauyi da aka samu a kan wannan batu dole ne kwamitin zattaswar jam'iyyar sai ya amince da hakan;
    d. Jam'iyyar za ta dauki kwararan matakai wajen gudanar da zabuka don qarfafa gwuiwar shigar qungiyar mutane da dama da ke cikin al'umma wadanda basu damu da wakilcinsu ba ga tsarin demokaradiyya, jam'iyyar za ta buqaci zaben 'yan takara wadanda ke wakiltar al'ummomin jinsi daban-daban har da naqassasu, da ma inganta samun shigar masu matsayi a fannoni ayyuka;
    e. Tsarin zaben zai kasance ne mai baiwa daukacin 'ya'yan jam'iyyar dama iri daya wato daidai wadaida tare da la'akari da irin matsalolin da qungiyoyin da suka nuna sha'awarsu ta shiga zaben ka iya fuskanta kuma a kowanne zaben zai kasance ne bisa tsarin mutum daya quri'a daya.
    f. Qa'idoji da sharuddan tafiyar da zabukan za su kasance ne masu saukin tafiyarwa ga bangarorin jam'iyyar

3. Ta la'akari da takardar tsare-tsare dake da aka ayyana a sashi na 52(a) da (b), na wannan kundin tsarin mulkin jam'iyyar za a yi amfani da ita ne kamar haka:
    a. Majalisar dattawar jam'iyyar ta jiha za ta kasance masu ikon amincewa da tsaida duk wani dan jam'iyyar da ke son fitowa takarar muqaman kansila ko shugaban karamar hukuma qarqashin jam'iyyar;
    b. Kafin duk wani zaben muqaman jam'iyyar ko na dan majalisar dokoki, sai majalisar dattawan jam'iyyare ta amince ta hannun kwamitin zattaswar jam'iyyar na jiha da ya samar da cewar wani tsarin dokar za ta fara ne tun daga matakan gunduma;
    c. Kwamitin zattaswar jam'iyyar na qasa shi zai kasance mai ikon amincewa da duk wani dan jam'iyyar da ke neman a tsaidashi takarar muqaman dan majalisar dokokin ta qasa ko muqaman gwamna ko shugaban qasa ko mataimakin shugaban qasa kamar yadda aka tanadar;
4. Ta la'akari da matakan da ke qarqashin sashi na 10(a), bangarorin jam'iyyar da suka fusata ne za su kasance wadanda za a buqaci neman afuwarsu ga kwamitin amintattun jam'iyyar.
5. Zai kasance akwai wa'adin shekara daya na zama dan' jam'iyya kafin la'akari da wani dan jam'iyyar da zai kasance wanda za'a nada a muqaman siyasa, amma ba tare da sabawa hukumar da abin ya shafa ba.
6. Amma a inda aka sabawa kwamitin tsare-tsaren wajibi ne ya samu amincewa da babban kwamitin zattaswa, tare da kwamitin zattaswa na qasa qanda zai kasance madakata.
7. 'Yan takaran neman muqaman jam'iyyar wajibi ne su kasance sun mallaki aqalla takardar shedar kamala makarantar sakandare kafin samun cancantar tsayawa takara. Amma buqatar irin wadannan takardun shedar ilimi ba za su kasance wajibi ba a matakin gunduma.
8. Jam'iyyar za ta kasance mai qarfafa gwuiwar zaben matasa ne a muqaman gwamnati.

**BABI NA TARA (9)**

TSARIN SAMAR DA KUDADE

58

1. Zai kasance akwai wani tsarin samarwa jam'iyyar kudaden shiga ta hanyar harajin da kowanne dan jam'iyyar zai biya, kamar haka:
    a. Harajin zama dan jam'iyyar daga 'ya'yan jam'iyyar;
    b. Tsarin samun kudade daga ayyukan da jam'iyyar tayi;
    c. Ta tsarin karbar gudummawa; ko
    d. Karbar kyaututtuka da gudummawar kudade daga qungiyoyi da sauran jama'a kamar yadda buqaci hakan;
    e. Samun amincewar karbar rancen kudade daga kwamitin zattaswar jam'iyyar na qasa; da
    f. Sauran makamanta wadanda kudaden haraji da doka da baiwa jam'iyyar damar karba;
2. Kudaden zama dan jam'iyyar zai kasance ne naira dubu biyu da dari hudu (N2,400) duk shekara, ka zalika wannan adadin kudaden zai danganci amincewar kwamitin zattaswar jam'iyyar na qasa ta hanyar la'akari da shawarwarin da aka yanke na kudaden da za a rinqa amincewa da su lokaci zuwa lokaci a babban taron jam'iyyar na qasa da kowanne dan jam'iyyar zai biya.
3. Wadanda kudaden za su rinqa biyansu ne a kan lokaci da aka qayyade tare da sanyasu a tadin shedar zama dan jam'iyya.
4. Don wata manufa ta inganta hanyoyin samun kudaden shigan jam'iyyar, daukacin zababbu da nadaddun 'ya'yan jam'iyyar maza da mata za su kasance masu biyan karin wadannan kudaden harajin da ke biye.
    a. Masu riqe da muqamai zababbu a majalisar dokoki (na fallan gwamnati uku) za su rinqa biyan kashi goma cikin dari (10%) na tsurar albashinsu na shekara.
    b. Nadaddun jami'an gwamnati (a fallayen gwamnati uku) su ma za su rinqa biyan kasha goma cikin dari (10%) na tsurar albashinsu na shekara;
    c. Sai jakadu (Ambassadors) su ma kasha goma cikin dari (10%) na albashinsu na shekara.
    d. Shugabannin hukumomi da wakilar a matakin gwamnatin tarayya; za su rinqa biyan kasha ashirin cikin dari (20%) na tsurar alawus alawus dinsu.
5. Sannan sauran jama'a da magoya bayan jam'iyyar da ke amfana da jam'iyyar a matakan qasa, jiha da qaramar hukuma za a rinqa qarfafa gwuiwarsu wajen ganin suna bada gudummawarsu duk shekara ga jam'iyyar, kuma hakan sai yay i daidai da dokar tafiyar da wannan tsarin a lo kacin ba da gudummawar.
6. Hakanan ma kudaden za a samu wajen saida takardun cikewa na neman tsayawa takara (forms) zai kasance ne a wani bangaren samarwa jam'iyyar kudaden shiga.

KWAMITIN KUDI NA JAM'IYYAR NA QASA

59

1. Zai kasance akwai kwamitin kudi na jam'iyyar na qasa (NFC) da zai qunshi:
   a. Shugaba dan jam'iyyar , mai rikon amana da gaskiya;
   b. Wakilan jam'iyyar biyu (2) da aka zabo daga shiyyoyin siyasa shida (6) na qaasar nan; da
   c. Ma'ajin jam'iyyar na qasa; da
   d. Sakataren kudi na jam'iyyar na qasa; da

AYYUKAN KWAMITIN KUDIN JAM'IYYAR

2. Mai binciken kudin jam'iyyar na qasa shi zai kasance a matsayin skataren kwamitin.
3. Kwamitin kudin jam'iyyar na qasa zai tafiyar da ayyuka ne kamar haka:
   a. Shirya wata liyafar bude assusun neman kudi na shugaban jam'iyyar na qasa, a inda mahalarta liyafar abokai da wakilan jam'iyyar za su biya wani abu daidai da yadda aka tsara da sauran kudade da kwamitin za azan a shirya liyafar cin abinc in daren.
   b. Duqufa sauran wasu aikace-aikacen samarwa jam'iyyar kudade da tallafi bisa bin dokokin da aka gindaya wa kwamitin akan batun.
   c. Tabbatar da bunqasa da dorewar hanyoyin samun kudaden shigan jam'iyyar bisa tanade-tanaden wannan kundin tsarin Mulki da sanya hannu jerin jam'iyyar a harkokin da suka shafi bangaren tsaro na gwamnati da kamfanoni da samar da jerin gidaje; da
   d. Kafa wani kasuwanci da bai starin sabawa duk wani tabade-tanaden kundin tsarin mulkin Nijeriya ba da na wannan kundin tsarin mulkin jam'iyyar.
4. Za a samar da wani kwamitin kudin jam'iyyar na jiha bisa dokokin da suka kafa na qasa wanda kuma ayyukansa ba za su sako ba da na kwamitin kudin jam'iyyar na qasa ba.

IKON KARBAR RANCE

60

1. Karbar rance ta kowacce hanya don cimma wasu wajibabbun ayyukan jam'iyyar da wannan kundin tsarin mulkin ya tanadar zai rinqa kasancewa ne bisa amincewar kwamitin zattaswar jam'iyyar na qasa.
2. Bisa tanade-tanaden wannan kundin tsarin mulkin jam'iyyar na qa'idojin shedar gaskiya na tafiyar da duk kayayyakin jam'iyyar za ta rinqa sanya kudadenta ne a duk wasu aikace-aikace ne bisa amincewar kwamitin zattaswar jam'iyyar na qasa.

TABBATAR DA GASKIYA DA RIQON AMANA WAJEN TAFIYAR DA HARKOKIN KUDIN JAM'IYYAR

61

1. Don tabbatar da gaskiya da riqon amana wajen tafiyar da harkokin kudin jam'iyyar, kwamitin zattaswar jam'iyyar na qasa zai samar da wasu qa'idoji da tsari da za su yi jagorancin tafiyar da harkokin kudi na jam'iyyar a dukkan matakai.
2. A matakin qasa kuwa, shugaban qasa tarayyar Nigeriya, da ya kasance dan' jam'iyyar zai rinqa tabbatar da ganin ana bin tanade-tanaden wannan kundin tsarin mulkin a bangaren da ya shafi biyan kudaden haraji na daukacin masu riqe da muqaman siyasa nadaddu yayin da shugaban majalisar dattawa da shugaban majalisar wakilai ta tarayya a matsayinsu na shugabanni n majalisar dokoki su kuma su rinqa tabbatar da ganin daukacin wakilan jam'iyyar na majalisan dokokin na qasa na bin tanade-tanaden wannan kundin tsarin mulkin jam'iyyar.
3. A matakin jiha kuwa, gwamnan jiha dan jam'iyyar ne zai rinqa tabbatar da ganin ana bin tanade-tanaden da suka shafi biyan kudaden haraji da wannan kundin tsarin ya dorawa masu rike da muqaman siyasa da aka nada a jihar, yayin da shugaban majalisar dokikin jiha dan' jam'iyyar shi kuma ya tabbatar da ganin wakilan majalisar dokikin 'ya 'yan jam'iyyar na kiyayewa da tanade-tanaden wannan kundin tsari mulkin.
4. A matakin qaramar hukuma kuwa, shugaban majalisar qaramar hukumar wanda yake a matsayin dan' jam'iyyar ne zai kasance mai tabbatar da ganin, masu riqe da muqaman siyasa da aka nada a qaramar hukumar na kiyayewa da tanade-tanaden wannan kundin tsarin mulkin na biyan kudaden zama dan' jam'iyyar, sai kuma shugaban majalisar dokiki na qaramar hukuma ta tabbatar da bin tanade-tanaden kundin mulkin a tsakanin wakilan majalisar na qaramar humar 'yan jam'iyyar.

ASUSUN BANKUNAN JAM'IYYAR

62

1. Jam'iyyar za ta bude asusun ajiya ne na banki a birni da yankunan da shalkwatocinta ke da zama, sannan a inda babu bankuna za ayi amfani da bankunan da jam'iyyar ke ajiya mafi kusa da wuraren.
2. Kwamitin zattaswar jam'iyyar na kowanne mataki ne zai kasance mai yanke shawarar bankin da za a yi amfani da shi wajen bude asusun ajiyan jam'iyyar.
3. Ba da ikon amfani da asusun ajiya na banki da sauran harkokin tafiyar da kudade sai ya samu sa hannun wadannan jami'an jam'iyyar kamar:

a. Sgubagan jam’iyyar na qasa ko takwarorinsa na matakan jiha da qaramar hukuma da na gundumomi;
b. Sakataren jam’iyyar na qasa ko takwarorinsa na matakan jiha ko qaramar hukuma da na gundumomi;
c. Ma’ajin jam’iyyar na qasa ko takwarorinsa na matakan jiha da qaramar hukuma da na gundumomi.

Wannan tanadin dokar na nufin babu yadda za a iya ciro kudade ko sakawa a asusun ajiyar jam’iyyar ba tare da sa hannun shugaban jam’iyyar na qasa da takwarorinsa na sauran matakan ko sakatare da ma’ajin jam’iyyar na qasa na sauran matakan ba.

<u>BINCIKEN ASUSUN AJIYAN JAM’IYYAR NA BANKUNA</u>

63

1. Kwamitin zattaswar jam’iyyar na qasa shi zai nada wani tsayayyen kwamitin kwararrun akantoci da zai rinqa binciken asusun ajiya na jam’iyyar na bankuna duk shekara tare da gabatar da rahoton bincikesa gay an jamiyyar.
2. Hakanan ma kwamitin zattaswan jam’iyyar na jiha da qaramar hukumar zasu kafa irin wannan tawagar ta kwararrun akantoci da za su rinqa binciken asusun ajiyar jam’iyyar duk shekara tare da gabatar da rahotonsu ga tarukan manyan jam’iyyar na matakai daban-daban.

**BABI NA GOMA (10)**

HANYOYIN LADAFTARWA

64

1. Bisa tanade-tanaden wannan kundin tsarin mulkin zai kasance akwai wani kwamitin ladaftarwa na jam'iyyar a kowanne matakin jam'iyyar da zai qunshi daukacin wakilan majalisar dattawan jam'iyyar na matakin jiha da daukacin wakilan kwamitin am intattu da ke da shedar da'a da martabada za su kasance masu kariyar doka.
2. Kwamitin ladaftarwan, kwamitin zattaswa da tsare-tsaren jam'iyyar ne zai nada.
3. Kwamitin zattaswar a kowanne matakin jamiyyar da zai iya dakatar duk wani dan jam'iyyar da aka kama da laifin rashin da'a da sauransu har tsawon lokaci da bai wuce wata daya (1) ba bayan bincike da zaman sauraren ra'ayi akan batun zabe a wanda aka dakatar din zai rasa damarsa ta tsayawa takarar kowanne zabe kuma za a turashi zuwa kwamitin ladaftarwar jam'iyyar.
4. Idan ana zargin wani dan jam'iyyar da aikata wani laifi, kwamitin ladaftarwar jam'iyyar zai kasance mai sanar da dan jam'iyyar da ake yi masa da wurin da lokacin sauraran qarar laifin da ake zarginta/sa da shi a rubuce.
5. Duk dan jam'iyyar da ya bayyana a gaban kwamitin ladaftarwar jam'iyyar, za a bashi damar gabatar da laifin da ake zarginsa da aikatawa a baki ko a rubuce da kansa ko ta hannun lauyan daya zaba kuma za a barshi ya kira shaidu.
6. Duk matakin da aka dauka na ladaftar da wani dan' jam'iyyar da ake zargi da aikata laifi, idan har ba a sanar da shi laifinsa ba kuma a bashi damar kare kanshi ba, za a rushe wannan matakin da watsi da shi.
7. Baya ga wannan tanade-tanaden ladaftarwar, duk wani batu makamancin haka, ba ruwan kwamitin zattaswar jam'iyyar na kowanne mataki, amma sai dai idan irin wannan al'amri ya shafi wani wakilin kwamitin zattaswa na qasa ko mataimakan gwamnoni ko wakilain majalisar dokoki na qasa, kwamitin zattaswar jam'iyyar na qasa zai lura da duk wani daukar matakin ladaftarwar.
8. Kuma wannan kundin tsarin mulkin ya tanadar da cewa babu abin da zai sa ayi watsi ko ajiye qarar da aka gabatarwa kwamitin zattaswar jam'iyyar na qasa a game da wani mutum ko ma menene.

## LAIFUKA DA HUKUNCI

65 Bisa tanade-tanaden wannan kundin tsarin mulkin jam'iyyar na da cikakken ikon hukunta duk wani dan jam'iyyar da aka kama da laifin:

1. Takewa ko sabawa tanade-tanaden kundin tsarin mulkin da turbar jam'iyyar;
2. Furtawa ko aikata duk wani abu da ka iya haifar da gaba ko tashin hankali ko rigima a jam'iyyar;
3. Qin biyayya ko nuna rashin kulawa ga duk umurnin doka na jam'iyyar ko na wani bangare ko jami'in jam'iyyar.
4. Rashin gaskiya, ga jam'iyyar ko wakilanta;
5. Qaurace wa taruka da ayyukan jam'iyyar;
6. Fadawa ayyukan cin amanar jam'iyyar;
7. Nema ko karbar muqaman siyasa na gwamnatin wata jam'iyya da ba jam'iyyar Youth Party ba;
8. Aikata ba daidai ba a taruka ko gangami ko a wasu ayyukan jam'iyyar
9. Fadawa ayyukan da ka'iya shafar 'ya'yan jam'iyyar ko haifar da rashin zaman lafiya da ta ke doka ko shafar harkokin jam'iyyar.
10. Yada rashin jituwa a cikin jam'iyyar ko raba kawunan bangarorin jam'iyya na kowani mataki;
11. Qarfafa gwuiwar yin tawariya ko shiga wani rukunin jam'iyyar da ke assasa sunan jam'iyyar da sunan da ba wannan kundin tsarin mulkin ya tanadar ba;
12. Shiryawa ko horaswa ko qarfafa guiwar a shirya ko horas da duk wani dan jam'iyyar ko qungiya don hadda sa rikici da rashin jituwa ko ma dul wani nau'in cin zarafin da sauran;
13. Farkewa da matakan kotu kan duk rikici ko wani batu da ya shafi 'yanci da ayyukan duk wani dan jam'iyyar ba tare da la'akari da hanyoyin shawo kan lamarin ba da samar qarwashin tanade-tanaden wannan kundin tsarin mulki.
14. Gazawa ko qin yin aiki kan duk wani koqe-koke qo qara ko roqo akan lokaci;
15. Shiga gudanar da ayyukan da za su zubar da mutuncin jam'iyyar idan manyan mutane da ke aikin al'umma.

**HUKUNCI**

66

1. Duk dan jam’iyyar da ya aikata laifukan da aka jero a sashi na 65 na wannan kundin tsarin muklin zai fuskanci daya ko biyu daga cikin wadannan hukunce-hukunce da ke tare:
    a. Qin amincewa;
    b. Tara;
    c. Dakatarwa daga ofis;
    d. Haramcin riqe kowanne ofishin jam’iyyar;
    e. Tsigewa daga offis;
    f. Kora daga jam’iyyar
2. Bisa tanade tanaden sashi na XIV na wannan kundin tsarin mulkin, kwamitin zattaswar jam’iyyar na kowanne mataki zai kasance mai ikon yanke shawarar daukar matakin ladaftarwa kan kowanne dan jam’iyyar a wannan mataki.
3. Bisa tanade-tanaden ladaftarwa da ke tattare cikin wannan kundin tsarin mulkin babu kwamitin zattaswar jam’iyyar na kowanne mataki da zai dauki alhakin tafiyar da batun ladaftar da wakilin kwamitin zattaswar jam’iyyar na qasa ko shugaban qasa da mataimakin shugaban qasa da gwamnanoni da mataimakan gwamnoni da minitoci da jakadu dsa masu ba da shawara ta musamman ko ‘yan majalisun dokoki da ke jam’iyyar face kwamitin zattaswar jam’iyyar na qasa.
4. Kwamitin zattaswar jam’iyyar kan ladaftarwa zai kasance mai ikon samarwa da dokar matakan ladaftarwa akan kowanne wakilin kwamitin zattaswa ko masu riqe da muqaman gwamnati da sauran ‘ya’yan jam’iyyar.
5. Bisa tanade-tanaden wannan kundin tsarin mulki, kwamitin zattaswa r jam’iyyar na qasa shi zai kasance mai qarfin ikon sallamar duk wani dan jam’iyyar da aka kama da aikata laifin rashin da’a da aikata ba daidai ba wanda ka’iya zubar da martabar jam’iyyar.

## HANYOYIN WARWARE MATSALOLI

67

1. Idan dan jam'iyya ya fusata, sai ya miqa kansa ga hukumomin da suka kamata.
2. Idan bai gamsu da hakan ba, sai a daukaka qararsa zuwa ga uwar jam'iyyar mafi qoli.
3. Daukacin qararraki wajibi ne a kamala duba su akan lokaci kuma cikin hanzari kuma wa'adin tafiyar da wadannan qararrakin ba za su wuce makonni biyu ba kafin miqa qararrakin.
4. Kwamitin zattaswar jam'iyyar na qasa shi zai kasance mai cewa ta qarshe akan duk wani qorafi na ga zawa da nuna rashin ko inkula na aikki a kan rahotannin qorafe-qorafen

**QARARRAKI**

68

1. Duk wani dan jam’iyyar da ya fusata sakamakon wani mataki da bangaren jam’iyyar ko jami’in jam’iyyar suka dauka a kanshi, yana da ‘yancin daukaka qararsa ga bangaren jam’iyyar qoli cikin kwanaki sha hudu (14) na daukar matakin
2. Bangaren kula da qararrakin zai rinqa la’akari da qararrakin ne cikin kwanaki ashirin da daya (21) daga lokacin da kwamitin zattaswar jam’iyyar kan tafiyar da wannan batu ya karbi qarar.

**BABI NA SHA DAYA**

**BANGAREN BINCIKEN TSARE-TSARE**

68

1. Zai kasance akwai wani bangaren binciko da tsare-tsare na jam'iyyar Youth Party da za'a rinqa kira da suna Youth Party Research & policy Unit; wanda zai kasance sashin tsare-tsare dabaru da ilmantarwa na jam'iyyar Youth Party kuma shi ke da alhakin:
    a. Qarfafawa da shirya dabarun cigaba da karbar shawarwari a tsakanin jam'iyyar musamman
    b. Samar da tsarin karbar irin wadannan shawarwari da tabbatar da ci gaba da tofa albarkacin baki akan dabarun
    c. Samar da ci gaba da hanyar amfani da kwararrun bangarori a muqaman fannoni na matakan qasa
    d. Gabatar da ra'ayoyin jam'iyyar ga sauran bangarori da ba na jam'iyyar ba, jam'iyyun siyasa da qungiyoyin da ke Nijeriya da ma na sauran qasashen waje.
    e. Tuntubar qungiyoyin qasashen waje don buqatar fadada manufofin jam'iyyar;
    f. Amincewa da wallafar manufofin jam'iyyar;
    g. Shirya maida manufofin wucin gadi muhimman batutuwa, kuma wadannan manufofin za su cigaba da kasancewa manufofin jam'iyyar amma sai idan har kwamitin zattaswar jam'iyyar ya amince da rahoton da suka yi wa wannan kundin manufofi da aka gabatar nata kariya;
    h. Samar da bayanan manufofin da aka buqata a aiwatar da qa'idojinsu da anince da su tuni.
2. Bangaren bincike da tsara dabarun shi zai kasance mai alhakin shirya muradun jam'iyyar na manyan zabuka, kuma yana da ikon tuntube shi sannan a wani yanayi da aka samu rikicin bayan wannan tuntuvar ta doka da abin ya shafa wajen shawo kan batun da ke tattare a muradun babban zaben na kowacce jiha.
3. Bangaren bincike da tsara dabaru zai kasance mai karfin ikon kafa tawagar tafiyar da tsare-tsare wanda wakilansa ba lallai sai wakilan bangaren ba ne za a nada shugaba,

kuma a buqaci tuntuba da shugaban wakilan tawagar za su rinqa kasancewa masu bada manazarta idan buqatar hakan ta taso.

4. Bangaren bincike da tsara dabaru zai kasance ne mai kwamitin gudanarwa na gwamnoni da wakilansa da basu wuce mutum sha biyar (15) bawanda kwamitin zattaswar jam'iyyar zai nada da aikinsa zai kasance tsara dabaru da manu fofin jam'iyyar.
5. Sakataren bangaren bincike da tsara dabarun jam'iyyar na qasa shi zai kasance shugaban kwamitin gudanarwa a bangaren binciken.
6. Babban daraktan kwamitin gudanarwa shi zai kasance mai alhakin tafiyar da harkokin bangaren nay au da kullum kuma zai kasance mai karbar umurni daga kwamitin gudanarwar bangaren
7. Babban daraktan bangaren zai kasance ne mai wa'adin shekaru biyar na sabunta wa'adinsa ko akasin haka.
8. Bangaren shi za a dorawa alhakin shirya tarukan bita da na ilmantarwa da bada horo akan shugabanci, da tsarin mulkin jam'iyyar kuma zai zamto mai gudanar da wasu sauran ayyuka da kwamitin zattaswar jam'iyyar ka'iya dora masa.
9. Ayyukan bangaren zasu kasance ne daidai da reshensa da tanade-tanaden wannan kundin tsarin mulkin cikin batun duba sha'anin kundin jam'iyya kuma bangaren zai kasance ne mai miqa qoqon barar sa.

## SAKATARIYAR SADARWAR JAM'IYYAR TA QASA

70

1. Zai kasance akwai wata sakatariyar sadarwar jam'iyyar ta qasa wanda aikinta zai zamo maganta dangantakar jam'iyyar da kafafen watsa labarai da yada bayanai da binciken jama'a da tallace-tallace.
2. Sakatariyar sadarwar jam'iyyar ta qasa za ta kasance mai hada gwuiwa da bangaren bincike da manufofi wajen tsara dabarun sadarwa na jam'iyyar a kowanne mataki da samar da shirye-shiryen sadarwa da tafiyar aikace-aikacen jam'iyyar bisa amincewar kwamitin zattaswar jam'iyyar na qasa ta hannun sakatariyar sadarwar jam'iyyar ta qasa.

3. Daraktan yada labarai da kwamitin zattaswar jam'iyyar ya nada shi zai shugabanci sakatariyar sadarwar jam'iyyar ta qasa
4. Daraktan sadarwar jam'iyyar na qasa zai kasance mai biyayya ne ga kwamitin zattaswar jam'iyyar na qasa ta hannun sakataren yada labaran jam'iyyarr.
5. Za a kafa kwamitoci sadarwar jam'iyyar a kowanne matakin jihohin Nijeriya don tafiyar da irin wadannan aikace-aikacen da kwamitin zattaswar jam'iyyar na qasa ya amince.

## BABI NA SHA BIYU

## SAURAN TANADE-TANADE DABAN-DABAN

71

1. Jam'iyyar za ta kasance ne a matsayin wata hukuma da za ta shigar ko a shigar da takara da kafin ikon mallaka, da riqe kayayyakin da akai yarjejeniya akan su da tafiyar da daukacin sauran manufofi da qudirori da kare kayayyaki da manu fofin 'ya'yanta.
2. Jami'an jam'iyyar na qasa ne kadai za su kasance masu ikon samar da duk wata dangartakar shara'a ga jam'iyyar.

## NANNADE KO BAYYANA SIRRIN JAM'IYYAR NA BAI DAYA

72. Zai kasance akwai wuraren nade daukacin bayanan sirrin jam'iyyar wanda za su kasance qarqashin sakataren jam'iyyar na qasa

## RANTSUWAR SHIGA OFIS

73. Duk wani mutum da aka zaba ko nadashi a muqamin riqe da ofishin jam'iyyar, sai an rantsar da shi kamar yadda aka tanadar a babi na daya na wannan kundin tsarin mulkin, da harshen ta/ya fi fahimta a gaban kwamishinan bada rantsuwa.

## GARANBAWUL

74

1. Jam'iyyar za ta kasance mai ikon yi wa wannan kundin tsarin mulkin gyaran fuska da zai zama sahihi, sai qudirin yin hakan ya sami amincewar kashi biyu bisa uku ($^2/_3$) na mafi rinjayen wakilan jam'iyyar da suka haxa da quri'ar yin haka a babban taron jam'iyyar na qasa.
2. Za a rinqa baiwa sakataren jam'iyyar na qasa wa' adin buqatar yiwa kundin tsarin mulkin jam'iyyar gyaran fuska ne da aqalla watanni biyu (2) kafin ranar gudanar da babban taron jam'iyyar kuma wa'adin zai kasance ne a rubuce wanda tsarin mulkin garambawul da dalilan yin gyaran fuskan.
3. Da zaran sakataren ya karbi takardar wa'adin yiwa kundin gyaran fuska shi kuma sai ya tabbatar da ya isa kowanne reshen jam'iyyar na jiha don yadawa da aqalla wata daya kafin ranar babban taron jam'iyyar na qasa.

## FASSARA

75

1. Duk wata tambaya akan ma'anar wani sashi ko jadawali da ke qunshe a wannan kundin tsarin mulkin, za a dangana ne da kwamitin jam'iyyar na qasa wanda fassararsa zata zamto qarshe.
2. A wannan kundin tsarin mulkin jam'iyyar:
   a. "Congress" na nufin wani babban taro ko zama inda wakilan jam'iyyar na kowani mataki za su gana don tattauna da musayar ra'ayi ko daukar mataki da zattas da shawarwarin gudanar da wasu harkokin jam'iyyar.
   b. "constitution" na nufin kundin tsarin mulkin Jam'iyyar;
   c. "Delegates" na nufin wakilan jam'iyyar na kowanne matakin rassan jam'iyyar;
   d. "Direct Primaries" na nufin wani tsarin taron da zai rinqa gudana a kowacce gunduma a inda daukacin 'ya'yan jam'iyyar masu rigista za su halarta don zaben dan takarar jam'iyyar da zai fafata a zabukan neman ofisoshin gwamnati.

e. "Fund" sun qunshi kudade da sauran abubwa masu gida rana;
f. "He or She" ya qunshi jinsin namiji ko mace;
g. "Local Government Area" na nufin yankin qaramar hukuma kamar yadda yak e a sashi na 7 da jadawali na biyu na kundin tsarin mulkin Najeriya na shekarar 1999 da aka yi wa gyaran fuska.
h. "Month" na nufin kalandar wata-wata;
i. "National Convention" na nufin wani babban taron jam'iyyar Youth Party na matakin qasa wanda ko da cewa ta qarshe na jam'iyyar kuma a nan ne ake warware duk wasu matsaloli da batutuwar da suka shafi jam'iyyar da zaben dan takarar shugaban qasa da sauran jami'an masu neman muqaman gwamnati a matakin qasa;
j. "National" wannan na nufin matakin tarayya kamar yadda hakan ke qunshe cikin kundin tsarin mulkin Najeria na shekarar 1999;
k. "State" na nufin wani shiyar siyasa kamar yadda yak e qunshe a cikin kundin tsarin mulkin Najeriya na shekarar 1999;
l. "The Party" na nufin jam'iyyar Youth Party,
m. "Ward" wannan na nufin yankin mazaba na qaramar hukuma da hukumar zabe ta qasa mai zaman kanta ta tanadar.
n. A indsa aka samu zobewar lambobin da aka buga a kwafuta a wannan kundin tsarin mulkin za a maida lambar ne zuwa lamba daya mafi dangantaka
o. "Zonal/zone" na nufin kowacce shiyyar siyasa kamar da Arewa maso gabas da Arewa ta Tsakiya da Arewa ta yamma da kudu maso gabas da kudu maso yamma da kudu maso kudu.

JADAWALI NA I

RANTSUWA

76. Ni,………………………………………….……na rantse zan zamo mai riqo da gaskiya da amana da biyayya ga jam'iyyar Youth Party da kundin tsarin mulkin Najeriya kuma zan kasance mai kiyayewa da kare kundin tsarin mulkin Youth Party da na tarayyar Najeriya. Allah ya taimake ni.

**JADAWALI NA II**

**RANTSUWAR KAMA AIKI A OFIS**

77. Ni……………………………………………na rantse tare da ba da tabbacin kasancewa mai gaskiya da biyayya ga jam'iyyar Youth Party kuma zan tafiyar da ayyukana iya bakin qoqari bisa gaskiya da riqon amana daidai da bin kundin tsarin mulkin jam'iyyar Youth Party bisa manufofi da muradun jam'iyyar da na tarayyar Najeriya; kuma zan jajirce wajen bunqasawa da cimma manufofi da qudirorin jam'iyyar kamar yadda ya ke qunshe a kundin tsarin mulkinta da muradunta; ba zan bari burina ya yi tasiri a kan na jam'iyyar ba wajen tafiyar da ayyukana; kuma a kowanne yanayi zan kasance ne mai gudanar da abin da ya dace ga daukacin 'ya'yan jam'iyyar da sauran jama'a bisa bin doka ba tare da tsoro ko shakku ba, ba zan yada ko bayyana wani sirri kai tsaye ba, ba tare da umurni ba, zan kasance mai sadaukar da kai wajen yi wa jam'iyya aiki da tabbatar da ingantuwar walwalar jama'ar Najeriya. Allah ya taimakeni.

JADAWALI NA III

ABUBUWAN GUDANARWA A WURIN TARUKA

<u>HARSHEN DA ZA A RINQA AMFANI DA SHI WURIN TARUKA</u>

78

1. Duk abubuwan da za a gudanar a wurin tarukan jam'iyyar a kowanne mataki za su kasance ne cikin harshen turanci wato ingilishi ko duk wani harshen Najeriya da mafiya rinjayen 'ya'yan jam'iyyar na matakai daban-daban suka fi fahimta.
2. Shugaba shi zai kasance mai jagorantar kowanne taron jam'iyyar, in baya nan, sai mataimakin shugaba ya shugabanci taron in kuma babu mataimakin shugaba sai 'ya'yan jam'iyyar da suka halarci taron su zabi wani dan jam'iyyar daga cikinsu don jagorantar taron.
3. Qa'idoji da sharuddan gudanar da kowanne irin taron jam'iyyar, zai kasance ne bisa amincewar majalisar zattaswar jam'iyyar na qasa lokaci zuwa lokaci.

JADAWALIN NA BIYAR (IV)

QA’IDOJIN MA’AIKATA

79

1. Ma’aikatan jam’iyyar za su kasance masu karbar umurni ne kai tsaye da ladaftarwa daga sakatariyar jam’iyyar na matakin qasa da jiha da na karamar hukuma da mazaba kuma daukacin qararraki kan batun ladaftarwa dana tafiyar da m ulki za a ji nginawa sakataren jam’iyyar na matakai daban-daban bisa bin tsarin da aka tanadar.
2. Daukacin ma’aikatan jam’iyyar za su kasance ne masu aiki da tanade-tanaden wannan kundin tsarin mulki da qa’idoji da sharuddan da matakan kwamitin zattaswa na qasa da sauran bangarorin jam’iyyar ne
3. Kuma duk mutumin da ke neman aiki a jam’iyyar sai ya zama dan jam’iyyar.
4. Duk ma’aikacin jam’iyyar da aka samu da aikata laifuka da ka’iya haifar da rikici ga jam’iyyar ko tsakanin jami’anta ko shiga ayyukan yi wa jam’iyyar zagon qasa ko nuna sakaci ga ayyukan jam’iyyar nan take za a cire ta/shi daga wannan matsayi.
5. Ma’aikata masu kunnen qashi za a rinqa basu damar kare kansu kafin daukar matakin ladaftarwa akansu.
6. Babu wani ma’aikacin jam’iyyar da zai nemi fitowa takarar zave, sai idan ta/ya ajiye muqaminsa wata daya kafin ranar zaben.
7. Biyan ladar aiki da sauran sharuddan aiki na kowanne ma’aikacin jam’iyyar zai kasance ne bisa la’akari da:
    a. Ma’aikata qasa da babban taron jam’iyyar na matakan qasa da amincewar kwamitin zattaswar jam’iyyar na qasa;
    b. Ma’aikatan jam’iyyar na matakin jiha ta hannun tarukan jam’iyyar na jiha bisa amincewar kwamitin zattaswar jam’iyyar na jiha;
    c. Ga ma’aikatan jam’iyyar na matakin gunduma kuwa, ta hannun tarukan jam’iyyar na yankin qaramar hukumar bisa amincewar kwamitin zattaswar jam’iyyar na qaramar hukuma.

**FARA AIKIN WANNAN KUNDI**

Wannan kundin tsarin mulkin zai fara aiki ne a ranar asabar 29 ga watan oktoban shekarar 2017.

……………………………………… ……………………………………….

Shugaban Jam'iyyar na Qasa Babban Sakataren Jam'iyyar na Qasa